Junaid yayi murmushi yace " Gaskiya kai na daban ne yallabai!! Murmushi General yayi yace "domin kama me laifi kana buk'atar hikima ,domin samun hikimar kuma! Dole ne mutum ya zama me izza!! Hydar yana da izzar hikimar bazata gagara ba! Amini na shine Commander na makarantar Rusev Del Rio shi ruwa biyu ne ,d'an North America kuma d'an Russia!! Shi zai kula da komai!! "....Nan general ya musu sallama ya fice ..............

🖊️🏵️Mayjiddah ja'o🏵️🖊️
[10/20, 10:09 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻

🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
5️⃣1️⃣🎞️5️⃣5️⃣

```15 ¥EARS LATER```

Jirgin Russian Airlines ne ta sauk'a a airport na Singapore, daga waiting spot na airport d'in na hango wani mutum of about 49 yrs or so tsaye da wasu y'an mata guda biyar d'aya daga cikin su se faman Kutsawa take gaba tana lek'o wa wanda ak'alla zata kai 19-20 yrs , yayinda mutane ke k'ok'arin fitowa daga jirgin ,wani matashi na hango k'akk'arfan gaske ya saka jeans da shirt bak'a sai wata armless mai hula , hular ya janyo ya rufa a kansa hankan ya b'oye Kyakkyawar fuskar sa, kai a 'kasa yake tafiyar da gani fuskar sa babu alamar fara'a ko kad'an.......

" Habawa !! Ai bari kuji yaya na ne zai dawo shiyasa na gayyace ku kuzo mu tarbeshi yanzu shekara goma sha biyar kenan ban sa shi a ido ba! Kun ma san me? Ni yanzu ba gane shi ma zan yi ba ,sedai shi zai gane mu!!" Zainab kenan cikin harshen turanci take wannan maganar

Sandy ,daya daga cikin k'awayen nata hud'u ta zaro ido tace " huuh!!? Fifteen years? Why ? Don't he send you his pics or chat with you on skyp or something? " buge ta Zainab tayi da k'afa tace " Look who's talking! You think my brother went to an ordinary school? He's a well trained soldier now! In their school all sort of fun is not allowed they know nothing than to break the jaws of a criminal!! "

Duk k'awaye suka sa dariya ,Kim dake gefe ta ce " she's talking as if her brother is a real superhero! Stop boasting Beb!" Zainab ta take k'afar Kim ta watsa mata harara , Uncle Junaid dake gefe se yanzu ya juyo ya dubesu yace " Careful ladies this is not a park for you to joke and fool around.

Daidai lokacin ,Matashin ya iso wajen Sandy ta zaro ido waje " Wow !! Kya ladka hai!!! (What a guy) " Uncle Junaid na d'agowa suka had'a ido da Matashin

Cike da fara'a ya nufo inda yake tsaye ya rungume shi yana fad'in " Welcome my Soldier!! Murmushi ya sakar masa wanda da shi da dole babu maraba!! Yace thanks Dad!!

Da gudu zainab ta k'araso inda yake ta rungume shi tace " welcome home Bro!! " kallon ta kawai yake ya kasa bud'e baki ya amsa mata se recalling childhood d'in su yake ,finally k'anwar shi da kullum sedai suyi waya sun zo face to face da ita!!"

Sake shi tayi tana dariya ,shi kuwa wata y'ar guntun murmushi ne kawai a fuskar shi. Ta juya ta kalli su Sandy tace " Finally my bro is home!!

" Yaya! Wannan classmates dina ne ,wannan sunan ta Sandy from Bangalore India ,wannan kuma Kim from Hong Kong , wannan kuma sunan ta Aisha ,ai ita kwanan nan ta zo ma ,daga
```

Nigeria! Wannan kuma.......

Bata k'arasa ba Hydar ya furzar da iska daga bakin shi ya juya idanuwan shi yace " Anjali from Delhi India!!! "

Zainab ta zaro ido tace " Hanh!!! Yaya akayi ka sani!? Watso mata harara yayi yace " All press students have their identity card hanged on their neck!! Tun kafin ki fad'a duk na karanta! Idan na tsaya biye miki duk mutanen airport d'in zaki kirgo min kafin mu isa gida!!! ".

Zainab ,Aysha da Uncle Junaid suka sa dariya ,Ta juya ta kalli su Sandy tace " Let's go yaar !! My brother needs some rest!!" ....................

FBI (FEDERAL BUREAU OF INVESTIGATION) US HQ
8:00AM...........

Zaune take saman motar ta ,hannun ta rik'e da disposable tea mug se Burger tana ci tana kallon yanda mutane ke shiga da fita a headquarters d'in.
Magana tajiyo daga cikin motar wannan yasa ta yi saurin zubar da abunda take ci cikin trash can (kwandon shara) ta goge hannun ta da handkerchief sannan ta shiga motar.

"Jones where the hell are you? I've been waiting !!" Mutumin da ya k'ira ta da Jones ya ce " Am sorry Detective we've just got a murder case ,am right now at the central park in Fifth avenue " Tayi saurin cewa " alright I'll be on my way!! "

Tana katse wayar ta fisgi motar ta dau hanyar zuwa fifth avenue kamar yadda Jones ya sanar da ita!!.............

Ku biyo ni don jin ko Wacece ita........

🖊️🏵️ mayjiddah ja'o 🏵️🖊️
[10/20, 10:09 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
5️⃣6️⃣🎞️6️⃣0️⃣

A parking lot na central park tayi parking motar ta , hannu a aljihu take tafiya ,tana yamutsa Kyakkyawar fuskar ta kamar wanda taga wani abun kyama.....

Bata dad'e sosai ba ta iso wajen da Jones ya sanar da ita ,wajen duk a zagaye da motocin police da FBI , iya fad'in wajen da akayi kisan an zagaye shi da wani tape wanda aka rubuta "

do not cross , crime scene !" 🚧

Ta k'ark'ashin tape d'in ta sunkuya ta shige ,ta tsaya gefen wani bature " Wooah!! This is disgusting!! Bye the way do you have any info on his identity? "
Tana fad'a tana kallon gawar da ke kwance ,police photographer se daukar hoton sa suke da duk wani abu da ke wajen ,chan gefe kuma hannun mutumin ne a guntule a gefe shima wasu lab scientists suna ta nasu gwajegwajen ,wata daga cikin scientists d'in ta taho inda su Jones suke tsaye ta mik'a masa hannu suka gaisa

Jones ya dubi scientist d'in ya kalli kuma detective yace" This is the new detective! ASY KHALEEL!! "

detective Asy khaleel tayi murmushi ta mik'a mata hannu suka gaisa ,scientist d'in tace " Pleased to meet you miss Asy ! I am Grace Garcia! I work in the lab with the FBI too it will be great working with you? "

Murmushi Asy tayi sannan tace " Any thing so far from the side of the Victim? "

" Not yet detective! The body will be moved to the lab for autopsy and the reports will be ready within 24 hours!
But we found this extinguisher can here, and also the cap is somehow like somebody tried to open it with d teeth!"

Kai Detective Asy ta jinjina tayi gaba tana kalle kalle ,ta durk'usa gaban gawar wanda hannun shi yake dunkule ,daga tsakanin yatsun shi ta ga kamar zirin gashi ,a ranta tace " Tabbas in dai wannan gashi ne kenan saida yayi kokawa da makashin kafin ya kashe shi , har ya samu ya Fisgo gashin kansa!! "

Da sauri ta mik'e ta k'ira Agent Grace tace " there is a piece of hair in his hand ,hurry take the samples ,we need a DNA report " grace ta mik'e tace " alright detective it will be ready in six hours!!! Grace suka d'auki gawar aka sa
[10/20, 10:09 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
5️⃣6️⃣🎞️6️⃣0️⃣

A parking lot na central park tayi parking motar ta , hannu a aljihu take tafiya ,tana yamutsa Kyakkyawar fuskar ta kamar wanda taga wani abun kyama.....

Bata dad'e sosai ba ta iso wajen da Jones ya sanar da ita ,wajen duk a zagaye da motocin police da FBI , iya fad'in wajen da akayi kisan an zagaye shi da wani tape wanda aka rubuta " do not cross , crime scene !" 🚧

Ta k'ark'ashin tape d'in ta sunkuya ta shige ,ta tsaya gefen wani bature " Wooah!! This is disgusting!! Bye the way do you have any info on his identity? "
Tana fad'a tana kallon gawar da ke kwance ,police photographer se daukar hoton sa suke da duk wani abu da ke wajen ,chan gefe kuma hannun mutumin ne a guntule a gefe shima wasu lab scientists suna ta nasu gwajegwajen ,wata daga cikin scientists d'in ta taho inda su Jones suke tsaye ta mik'a masa hannu suka gaisa

Jones ya dubi scientist d'in ya kalli kuma detective yace" This is the new detective! ASY KHALEEL!! "

detective Asy khaleel tayi murmushi ta mik'a mata hannu suka gaisa ,scientist d'in tace " Pleased to meet you miss Asy ! I am Grace Garcia! I work in the lab with the FBI too it will be great working with you? "

Murmushi Asy tayi sannan tace " Any thing so far from the side of the Victim? "

" Not yet detective! The body will be moved to the lab for autopsy and the reports will be ready within 24 hours!
But we found this extinguisher can here, and also the cap is somehow like somebody tried to open it with d teeth!"

Kai Detective Asy ta jinjina tayi gaba tana kalle kalle ,ta durk'usa gaban gawar wanda hannun shi yake dunkule ,daga tsakanin yatsun shi ta ga kamar zirin gashi ,a ranta tace " Tabbas in dai wannan gashi ne kenan saida yayi kokawa da makashin kafin ya kashe shi , har ya samu ya Fisgo gashin kansa!! "

Da sauri ta mik'e ta k'ira Agent Grace tace " there is a piece of hair in his hand ,hurry take the samples ,we need a DNA report " grace ta mik'e tace " alright detective it will be ready in six hours!!! Grace suka d'auki gawar aka sa a ambulance suka wuce da shi.....,.........

Wata chick Asy ta hango ta tsaya jikin motocin su tana waya , Asy ta kalli Jones tace " And who is that young lady? " Jones yayi Murmushi yace " that!! ? She's a cop! Azeeza M.K by name , actually we did our training together working with her is a great deal am telling you!! "

Kai kawai Asy ta jinjina ,ta ciro wayarta tana danna wa tana taunar chewing gum, saida ta kusa isa parking lot d'in tace " Irin wannan jinin da yau ban ci abinci ba da se jiri ya d'ebe ni!! " karaf maganar se a kunnen AGENT AZEEZA
Ta zare gilashin idon ta tayi murmushi tace " shiyasa ban k'arasa wajen ba!"

Cikin sauri Detective Asy ta waiga tana kallonta da murmushi tace " Hello Agent Azeeza M.K !! ". Wani murmushi Azeeza ta sake tace " I like that! Har kin san suna na? Gaskiya ina son inga ina aiki da me zafin nama! ,it will be a pleasure working with you Detective Asy Khaleel!! "

Asy tayi wata y'ar murmushi tace " Same here!" Nan Asy ta bud'e motarta ta shige itama Azeeza ta shiga nata suka bar wajen............

🖊️🏵️ Mayjiddah ja'o🏵️🖊️

[10/20, 10:09 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🎞️6️⃣5️⃣

SINGAPORE.......

Hydar na hango cikin d'aki yana dressing up, ya d'ago wani bak'in vest zai sa Zainab ta banko k'ofar ko sallama babu tsabar surutu, " Lalalaalla!!!😳 kai amma yaya kai me k'arfi ne!! Your muscles are huge! And you got twelve packs also!!! 💪🏼 amma yaya wanne irin exercise kake yi! " duk a tare tayi maganar nan kamar wata zabiya!!

Shidai bai ce 'kala ba se kallo da ido , da taga bai yi magana ba ta tab'e baki ta janyo laptop nashi ta kunna sai kuma ta juyo tana kallon shi " Yaya mene nasa password kuma ? Ni ka bud'e min! " nan ma bai kulata ba ya d'auki rigarsa yasa sannan ya zauna gefen gadon ,tana ta gwaje gwajen password duk ta kasa ta yi guntun tsaki, sannan ta kama zata rufe sai ya rik'e ,ya ya d'auki laptop d'in ya danna password sannan ya mik'a mata, duk ta gama dube duben ta babu wani game balle girly stuffs.

Don haka ta juya ta bashi baya ,ai kuwa duk wani Game da yake na Mata ne da themes duk seda tayi downloading tana yi tana dariya ,komai na system d'in ya koma pink wallpaper da sauransu, seda ta kusa gamawa da chaji sannan tayi mik'a, shi kuwa har bacci ma ya d'ebe shi , jona wa tayi a chaji ta d'auke rigar shi Armless da yazo da ita ta saka ta fice daga d'akin tana y'ar wak'ar ta 🎼🎧. Shi kuwa sam a gajiye yake bai ma san ta fice ba.........

K'arar wayar sa ce ta tashe shi daga nannauyan baccin da yake yi, ya mik'e da 'kyar ya d'auki wayar. " What? Kana nufin M.K yayi taking flight daga UK zuwa nan? Zai iya yiwuwa wani drug deal yazo yi , amma ba komai zan duba "

Daga d'ayan 'bangaren aka ce " Akwai wanda zamu had'a ka da ita ,tana investigation akan wani murder case, nan da gobe zan karb'i case d'in a hannu na , Sunanta Detective Asy khaleel , from The criminal intelligence agency (CIA) you have limited time do your best and bring back dat dog to Nigeria!! " idan muka samu Mk kamar Mun samu Don BK ne!!"

Hydar ya d'an yi ajiyar zuciya ya ce " Amma general! Aiki na zai tafi da mace kuwa?? I think

its better you let me do my part!" General yayi dariya yace " She's a woman like no other ,trust me bazata yi letting naka down ba! So do as I said!" Da 'kyar Hydar ya amsa yana Sosa 'keya sam ransa baya son aiki da mata   ya ajiye wayar ya mik'e yana kallon agogo sannan yace " They all are the same " talk too much and cry for a little thing!!"

Ya d'auki system nashi ya fita falo don duba wasu files ,me zai gani 🙄 duk an chanja masa komai ,gaba d'aya yama rasa ta inda zai fara ,wasu games kawai yake gani Barbie dress up games da sauransu 🤔
Ya d'aga gira sama ya yi tagumi yana kallon laptop d'in nashi kamar zai shige ciki ,ya ma rasa ta inda zai fara...

Bai ankara ba se ganin Zainab yayi tana ta manna masa stickers pink and blue masu kyau wasu na butterflies ne . da sauri ya d'ago laptop d'in ya juyo yana kallon aika aikan da tayi masa. Zai yi magana ta fara kyalkyata dariya ta cire wani sticker d'in ta manna masa a goshi yana ji yana gani. Tana yin abunda ya kawota ta mik'e jin k'arar motar Uncle Junaid yasa ta nufi k'ofar gida da gudu tana dariya...

Stickern goshin nasa ya cire yana dariya ,yana d'aga kai sama yaga gidan ma duk se k'yal-k'yali yake duk tayi  masa kwalliya  ya rasa inda ma zai sa na hannun nasa kawai se ya maida goshin nasa yana dariya.... A hankali yace  " crazy little princess!😘............

Asy da Azeeza ne zaune cikin Office d'in babban su . ya dubi Asy yace " From now onwards your case will be investigated by me! Am sending you on a mission to Singapore , this is an order from the agency not from me ,you'll meet the President of the CIA he'll explain everything. " Ba dan ranta ya so ba tayi murmushi ta amsa da " yes sir!!" Ta Sara masa ta fice abunta........

Agent Azeeza ta yi murmushi ta mata sallama sannan ta fice se kunkuni take yi ,Jones da sauran ma'aikata kowa ya juya ana kallon ta yayinda take tattare important takardun ta daga kan table d'in ta zata fice............

SINGAPORE AIRLINES........

" Yaya wai ni waye muka zo d'auka ne? Gaskiya nifa zan yi latti inada lecture!!" Yana jin duk abunda take fad'a amma yayi turus ,da ta ishe shi da surutu ya kama hannun ta ya fara tafiya direct ya nufi inda ya ajiye motar sa ya bud'e ya saka ta aciki sannan ya zagaya ya shige ya ja motar ,ba tare da ya kalleta ba yace " Menene sunan schl d'in " tunzira baki tayi ta juya masa 'keya tana kallon hanya. Abun ya bashi dariya amma ya gimtse ya kama ID card nata ya duba ,sannan ya d'au hanya.
Bata ma san sun iso makarantar ba taji dai motar ta tsaya ta juyo ta watso masa kallo  shima kallon nata yake yi kafin yace " Ko dai ni zan miki lecturen ne ? Ki fita mana! " nan ne ta lura ma an iso makarantar , ta zaro ido waje ta hangame baki " Yaya ta ya akayi kasan makarantar? "

Mashigar makarantar ya nuna mata nan ta hango Sandy da Kim suna fita daga school bus yace ",su suka nuna min Hanya " dariya tayi tace " Ok Mr grumpy!! Se na dawo." Ta fice tana d'aga masa hannu shima ya d'aga mata hannu yana Murmushi sannan ta juya, a hankali tace " Shi daman yana dariya🤔"..................

🖊️🏵️Mayjiddah ja'o🏵️🖊️
[10/20, 10:09 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🕠🎞️7️⃣0️⃣

Taku take d'ai d'ai kamar bazata taka k'asa ba , jikinta sanye da top da kuma high waist skirt bak'i, ta yafa mayafi bak'i a kanta ,simple makeup indeed but gorgeous looking!!
Amma sedai daga ka ganta kasan ranta a b'ace yake ,seda ta fito daga airport d'in ta tari taxi tace "No 2 C.I Nagar " ba musu taxi driver yaja motar suka hau hanya.

Wayarta ta zaro daga purse nata tayi dialling wata number, a cikin yaren Hausa sukayi magana " Sir nikam wane irin mutum ne aka had'a ni da shi! He wasn't even at the airport to pick me off its totally disgusting seriously!! " Daga d'ayan bangaren aka ce " Come on Asy! Wannan mutumin fa ba mai sauk'in kai bane, kiyi hak'uri kawai dan zakiga abubuwan da suka fi haka ma! Just excersice patience bari zan masa magana yanzu zan ji dalilin rashin zuwan nashi......"

Wani tafkeken gida taxi drivan yayi pulling off( ya ja birki ) ,saida ta lek'o ta windown motar ta zare gilashin idon ta sannan tayi ajiyar zuciya ta mik'a wa drivern kud'in sa ,ya tsaya yana kallonta baki a sake , cikin yaren indianci ya ce " Madam! Yeh to dollar hai!!( madam but this is a dollars) ta juyo tana kallon shi ba tare da ta fahimci me yake fad'a ba ta tsaya tana kallon shi!!. Ganin ba wani ganewa tayi ba yasa ya zaro kud'i irin nasu daga aljihun shi ,yana dariya ya mik'a mata Dollar d'in ya juya zai tafi. A kasalance ta juyo tace " Excuse me !! But how about your money?? " Murmushi ya mata yace " Think of it as a free ride!!" Itama tayi dariya tace " thank you * yaja motar ya bar wajen.........

A hankali take dosan k'ofar gidan wanda bazance yana da gate ba se wani d'an guntun fence da flowers sun zagaye, chan gefe wata bak'ar Audi ce a ajiye gefenta kuma Highlander jeep k'irar Chevrolet Silverado saida ta gama k'are ma komai kallo sannan ta sa k'afa ta k'arasa cikin gidan.....

This is where the drama begins readers ,ko ya zata kaya tsakanin Asy da Hydar ? Shidai ya ma manta da zancen daukota daga airport!!!.........

🖊️🏵️Mayjiddah Ja'o🏵️🖊️
[10/20, 10:09 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
7️⃣1️⃣🎞️7️⃣5️⃣

Da k'afa ta tura k'ofar ta shiga , falon komai na ciki fari ne se kwalliyar da Mutuniyar ta masa na colours pink ,purple en lemon grn, chan kan wata sofa ja dake ajiye a wani fili k'asan stairs ta hango mutum kwance ,daga shi se vest da 3quater ya rufe fuskar shi da Magazine, direct wajen da yake ta nufa a lokacin da idanuwan ta suka ci karo da damtsen hannayen sa, ta ware ido tace " So huge really!! " ganin ya motsa yasa ta gyara tsayuwar ta da masifa ta isa inda yake ta fisge magazine d'in da ya rufe fuskar shi ta had'e rai kamar zakanya .

A hankali ya bud'e fararen idanuwan sa ya d'ora kan Kyakkyawar fuskar ta , wani Yarr tsikar jikin sa yayi tuni ya kauda kai gefe.
" How dare you!! Did you think i come here all the way from New York city to wait for you at the airport about two good hour s without you showing up?? " ta inda detective Asy ta shiga ba ta nan take fita ba tun Hydar yana jin ta har yaji kunnen shi na masa 'kara ,bai san lokacin da ya zabura ya mik'e ya bar wajen ba...

Naushi ta kai wa kujeran da ya tashi a kai tana huci kamar macijiya " wato ma wannan ya maida ni mahaukaciya ko?" Muryar Hydar ta jiyo daga bayan ta yace " Ni ban ce ke mahaukaciya bace amma tunda kin d'auka a hakan kawai ma ki d'auka hakan nake nufi " yana kai wannan ya ajiye mata glass of water a gabanta ya wuce stairs.....

Baki a sake ta bishi da kallo wani kullutu ya taho ya tokare mata mak'ogoro ta fisge Jakarta ta nufi upstairs, ta rasa ma inda zata shiga ,ita ba. Sanin gidan tayi ba kuma taga alama wannan d'an rainin wayon tasu bazata zo d'aya ba don haka ta shiga bud'e k'ofofi ,na farko tana bud'ewa duk pics ne na Disney princesses da fairies , ta juya idanuwan ta tace " Ahhhhh!! Wannan wanne irin abu ne!!! Wato har yara ma akwai a gidan na? Ni gaskiya sam bana son hayaniya!! " ta ja k'ofar ta rufe ta nufi d'ayar ,ita kam ma a bud'e take tana lek'a wa me zata gani??!

Hydar ne tsaye babu riga a jikin sa ya d'auki towel k'arami yana faman rataya wa a wuya. Zaro idanuwa tayi waje ta hangame baki " Wooowww!! What a body man!!" a hankali tayi maganar yanda ko ni da nake kusa da ita ban da 'kyar naji abunda ta fad'a, Hydar ya juyo ya nufo hanyar k'ofar ta juya taga babu wajen b'oyewa se ya ganta , nan ta sunkuyar da kai k'asa bata ankara ba se ji tayi ya rufe k'ofar sa kirif😃 ni kaina nayi mamaki like seriously ya akayi ya gane da mutum a bakin kofar bayan ba a gaban mirror yake ba ba kuma facing k'ofar yake ba...

Baki ta murguda ta juya tana dube dube ta hango wani d'akin ma a cikin wani d'an corridor

kamar zata je se kuma ta fasa nan ta ajiye akwatin nata tayi pillow dashi a nan bacci ya d'auke ta.......

AZEEZA...

Zaune take itada Jones suna hira ,wayar Jones ne tayi k'ara ya d'aga ba tare da yayi magana ba ya katse wayar ya dubi Azeeza ,itama kallon sa take yi kafin tace " Anything trending? " Murmushi yayi yace " the autopsy report are out! Also grace was able to get us the DNA results. Azeeza tayi murmushi tace let's go to the lab " nan suka mik'e suka nufi hanyar lab d'in..............

AT THE LAB.........

Grace Garcia na hango tare da su Azeeza suna ta tattaunawa , don haka na d'ebo takardu na na yi sand'a don jin me take sunna musu a amadun kunnen su 😂.

Cikin harshen turanci Azeeza tace " kina nufin wannan Cylinder d'in da hak'ori aka yi niyyar bud'ewa se kuma ya gagara, sannan ba'a samu wani thumb print ba a jiki? Grace ta gyad'a kai tace " Exactly!! Kuma ina so in sanar da ke cewa ba da bindiga aka yi kisan ba , akwai murder weapon, abunda akayi amfani da shi sharp object ne sosai kuma is made of pure iron , domin kuwa akwai gaurayen iron a daidai inda yankar ta fara, kuma sannan binciken da abokan aiki na suka yi ya tabbatar mana cewa ba cikin gaggawa aka kashe shi ba ,victim d'in seda ya jigata sosai ,duk wanda yayi Wannan kisan ba k'aramin me wayo bane ,bai bar traces na komai ba ,DNA result ya nuna cewa ba real gashin mutum bane a kanshi gashin doki ne ,kenan clue da muka samu na d'aya shine -Makashin yana da bald hair ne! Na biyu kuma the killer is left handed wato yana amfani da hannun hagu ,na uku kuma bashi da hak'ori guda d'aya canine teeth nashi is replace with a gold one ,ma'ana hakorin shi daya na gwal ne a lokacin da yake faman bud'e cylinder d'in hakorin ya fice ,wata'kila garin sauri kuma bai d'auka ba yayi gaba...........

Jones yayi shiru yace " zamu iya ganin cylinder d'in? Grace tayi murmushi tace " sure !! Why not ? Ta d'auko cylinder cikin wata y'ar rubber bag ta mik'a mishi ,wani code suka kwafa a jikin leaflet d'in jikin cylinder sannan sukayi wa Grace se anjima suka fice.............

Direct office suka koma ,wani abokin aikin su na zaune suka mik'a mishi code din Azeeza tace " Check this out buddy ,get us exactly from which shop this came from!" Ta juya ta kalli Jones tace " to find more clue's we must know exactly who bought this cylinder!!" Murmushi Jones yayi ya kurbi coffee............

ZAINAB......

Tana tashi daga school suka fito ita da su Kim , Wata farar bus ce tazo ta wuce fiiiiii da gudun tsiya ,zainab da idonta ya sauk'a a kan motar ta hangi wani d'an saurayi ta bayan motar da gani he's in trouble , se kokawa yake da wasu katti a cikin motan , Key d'in scooter ta wafce daga hannun Kim ta hau ,ko helmet babu ta fara zuga gudu tana bin bayan motar , speed d'in da tayi amfani da shi ya wuce speed limit na k'asar ,gashi tayi nisa da school scooten ya b'aci , gashi kuma police sun biyo ta saboda tayi breaking law ,na farko over speeding na biyu ta wuce lokacin da traffic light ya nuna alamar tsayawa. Sorry Young lady you will have to come with us to the station!! " cewar wata Yar sanda kenan . babu yanda Zainab ta iya haka ta bisu ta shiga motar amma duk idonta na kan hanyar da wannan motar tabi ,se sak'e sak'e take cikin ranta " Ko waye Wannan d'in kuma me ya musu suke torturing nashi haka???"

🖊️🏵️ Mayjiddah ja'o🏵️🖊️
[10/20, 10:09 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
7️⃣6️⃣🎞️8️⃣0️⃣

Hydar na hango zaune cikin office d'in yan sanda yana magana da wani babban su , ba'a jima ba aka fito da Zainab wani police ya mik'a mata Jakarta sannan tayi signing a wata takarda , shima Hydar yayi signing sannan suka fice....

Sim sim take tafiya kamar kwai ya fashe mata a ciki fuskar nan kamar zata yi kuka ,Hydar kuwa ko waiwayota bai ba kawai ya bud'e mata k'ofar mota ta shiga sannan shima ya zagaya ya shiga ya hau tuk'i ,moment of silence sukayi experiencing a mota har suka iso gida ,jira yake ta fita ya mayar da motar inda take amma ko motsawa batayi ba ,suna had'a ido ta fashe da kuka kamar wata little gal

A take fuskar Hydar ta sauya kala ya fita daga motar ya zagayo inda take ya bud'e k'ofar, hannun ta ya kama ya fito da ita waje gami da zaunar da ita a kan grass carpet da ya mamaye filin gidan shima ya zauna sannan ya ciro wayarsa yana videoing d'in kukan nata , cije lab'en ta tayi ta fara neman wafce wayar daga hannun shi nan suka fara zagaye gidan da gudu , Zainab tana karb'e wayar ta nufi d'akin ta da gudu ,nan ta wuce Asy a zaune tana game da wayarta , sam bata kulata ba ta shige da gudu tana dariya , da gudun shi ya taho babu birki ,bai ma kula da Asy ba ya shiga d'akin Zainab ,Zaune ya iske ta tana d'aukar hoto da wayar tashi ,shima shiga Yayi tana ta d'aukar su a tare chan da ya gaji ya d'an jingina da gadon. Yace " Baby! Me kika yi wa police ne? Nifa ban ma tsaya sauraron su ba " nan ta kwashe labarin abunda ya faru ta fad'a masa

Hydar ya mik'e yana cewa " You are just a student journalist! So baby I urge you stay your limit bana so kisa kanki a crime control ,wannan aikin mu ne na sojoji!!" Yana magana yana kashe mata ido ,Mik'ewa tayi ta Sara mishi " YES SIR!!!" dariya yayi yace " Kar ki fasa min

dodon kunne ,kunnen nashi takama ta ja sannan tace " Haba maza! Kai da kake Karin kumallo da bindigogi iri iri shine d'an wannan Muryar tawa zata fasa ma dodon kunne!?" Dariya ya fara yana Jan hancin ta ita kuwa se kallon shi take kafin tace " Ashe yaya kana dariya me sauti haka?"

Wata dariyar ce ta kufce masa yace " Me kika dauke ni ? Anyway kinga ni zan fita se na dawo ki ci abinci fa coz am not sure if I'll be back in tym" Kai kawai ta girgiza masa yayi kissing goshin ta ya fice........

A corridor d'in ya iske Asy se wani shan kamshi take yi ya d'auki trolleyn nata ya kai wani d'aki sannan ya fice ,har ya shiga mota bai ma san tana biye da shi ba se jin ta yayi ta shiga mota . Rai a had'e yace " Me kuma kike yi anan! " Ai an turo ni muyi aiki tare ne so idan har mutum irin Ka wanda ba son jama'a yake ba ya fita at this moment toh lallai ba karamin abu ne zai sa ya fita ba don haka na san aiki zaka ,kar kayi tunanin nima ina son yin aiki da kai ne wlhy nima na tsani Marar fara'a 😏"

Juyowa yayi yana kallon ta har ta idar sannan ya ja seatbelt ya d'aura, wayarsa ce tayi k'ara alamar message ya shigo yana dubawa yayi wata murmushi ta gefen fuska yace " That's my uncle!!" Sannan ya fisgi motar ya fice daga gidan , ita de se kallon shi take yi ,cikin ranta tace " Indeed a prince charming but a grumpy one as well! Always frowning his face!!" Se kuma tayi murmushi ta juya.

Bakin wani restaurant ya tsayar da motar tashi CHAUDRY DHABA FOODS " indian restaurant ne me kyaun gaske ,suna shiga yace table seven yake buk'ata ,ba musu wani Dan indie ya kaisu wajen sannan ya basu Menu ya tsaya , Hydar da idon sa baya kan Menu d'in yana ta dube dube ,wani table a gefen su ya hangi wasu mutane su biyu ,duk bak'ak'e ne kamr black Americans ,'kasa k'asa suke magana baka ma iya jin ko sautin maganar ,da sauri ya dawo da dubansa kan menu d'in ya dubi mutumin dake jira yace " Get me two bowls of bhel puri and a glass of tamarind juice , ba musu mutumin ya amsa yana kallon Asy da ta rasa me zata zab'a, Hydar yace " do you think am going to eat all the two bowls of bhel puri? One is for the young lady pls , murmushi d'an indian yayi ya kama gaban sa , Hydar ya mik'e kamar zashi wani waje da gangan ya shiga gaban wani waiter suka ci karo ya yi kamar zai fad'a kan mutane biyun nan ,a wayance ya jefa wani na'ura ta mouth piece a aljihun d'ayan su sannan ya mik'e yana apologising kamar ba ruwan sa. Nan mutanen suka cigaba da abunda suke yi yayinda ya saka earpiece d'in shi kuma a kunnen shi yana sauraron duk abun da suke fad'i!! " yana yi yana taunar Bhel puri hankali akwance , Bai ankara ba se ganin Asy yayi tana faman tofar da abincin daga bakin ta yace " Be careful young lady !! D'aya daga cikin abubuwan da suka tsana ne ,ka nuna abincin su babu dad'i!! " da sauri ta gyara zamanta tana kurb'ar drink d'in a hankali...

" Aaj tumhara akhri din hai! Mujhe bas ek caror rupee jahiye " (yau shine ranar ka ta k'arshe! Abunda kawai nake buk'ata shine caror rupee d'aya!!) Abunda yaji daya daga cikin wad'annan mutanen ke fad'a kenan shi kuma d'ayan yace " I'll get your money by 8:oo pm but pls don't hurt my son! Tell MK that I'll do whatever he says amma don Allah kar ya tab'a min d'ana .

Hydar ya kalli detective Asy yace " Ke y'ar k'auye tashi mu tafi dalla!!! " hararo shi tayi tace wace y'ar k'auyen? Malam ka iya bakinka!! " bai ma saurareta ba ya fice ya zauna a mota itama seda ta ga dama sannan ta fito  seda ta iso jikin motar yaja abunsa ya k'ara gaba 😂

Wani haushi ne ya tattaro ya tsaya mata a mak'ogoro tana ji tana gani ya tafi abunsa ,gashi ko alamar taxi bata gani ba ta je bakin bus stop ta zauna kan wani rest bench tayi tagumi ,wani bak'in cikin ma seda ta kira general wayar sa bata shiga ba...........

Afwan  readers kun Jini shiru ban da Ipya ne dats why  ,love yhu all😘

🖊️🏵️ mayjiddah ja'o🏵️🖊️
[10/20, 10:10 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🎱🎞️8️⃣5️⃣

CHINATOWN

A daidai mashigar wani hotel a Chinatown yayi parking yana zaune cikin motar har mutumin ya shiga ya gama abunda zaiyi ya fito , duk maganganun da yayi Hydar yana ji saboda mouthpiece da ya saka masa a aljihu , Hydar bai jira fitowar mutumin ba ya juya da motar shi zuwa inda ya bar Detective Asy Khaleel.

Zaune take ta d'aura fuskar ta a kan tafin hannu , iska me dad'i na kad'awa tana iya jin sautin mutane jifa jifa suna wucewa kowa da nashi purpose d'in. Birkin motar da taji a gabanta shine yasa ta d'agowa karaf suka yi ido hud'u da Hydar tsabar neman tsokana ya kashe Mata ido yanda abun ya matuk'ar bata haushi , 'kasa k'asa tace " Zan koya maka hankali ne!!"

Washegari......

A cikin gym na hango Hydar yana working out da gudu Zee ta shigo sanye da pyjamas nata d'auke da glass na fresh fruit juice " Good morning Bro!!" Ta fad'a tana neman wajen zama . sauk'owa yayi daga kam machine d'in yana share zufa da k'aramin towel yace " Morning Parrot! Yau kuma da wanne zamu Fara? Surutun naki ko kuma me?". Haba Bro nifa ba parrot bane! Yawwa yaya ni yau shopping Zan je! Kuma Kai zaka raka ni!

Hydar da ko kallon inda take bai yi ba yace " No sweetheart ina da ayyuka da yawa ,Kije ki kawai! Maybe some other time" had'e rai zee tayi tace
"Oooooh  come on soldier!! This is Singapore remember? You'll love it! Zamu zagaya kaga gari

muyi shopping and also have dinner out you'll meet a lot of people and see interesting.. ……...
Bata k'arasa ba Hydar yace " da wannan surutun naki da ma kawai zuwa kikayi kika shirya dan nasan yau in ban fita ba se kunnuwan nah sun fashe!"

Wani tsalle ta daka ta rungume shi tana fad'in" thank you !! Thank you!! Thank you!!!" Daidai lokacin Asy ta fito tana zagaya gidan , idanuwan ta karaf cikin na Zainab a take ta zaro ido tace " Masha Allah!! Yaya wannan ce bakuwar da mukayi? " Kai kawai ya girgiza Mata , da sauri ta sake wuyanshi zata je wurin Asy yayi saurin chafko hannun ta yace " you have just twenty minutes ki shirya ko in k'i fita shopping d'in" don haka zainab ta sa dariya ta nufi hanyar shiga cikin gida .

Tsuka Asy ta ja hannunta nannade a k'irjin ta tace " dad'in ta ma Muma muna da k'anne" kalaman ta sai a kunnen Hydar bata yi zaton yaji ba sam !se ji tayi yace " Mu gani a k'asa" yana Kai Wannan ya fice yana dariya.

Wani bak'in ciki ne ya tokareta a wuya jin kalaman sa ta murguda masa baki sannan ta k'arasa cikin gym d'in..........

Jeeddah jao🏵️
[10/20, 10:10 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ESAH JA'O 💔🔪( 2016)
8̶6̶🎞️9️⃣0️⃣

Bayan sun gama breakfast wata number ta k'ira wayar Asy ba tare da tayi magana ba ta katse wayar sannan ta nufi hanyar d'akin ta , a daidai corridor d'in taci Karo da Zainab ta kammala shirin ta zata nufi d'akin Hydar , " Hey bakuwar mu! Kema zaki bi mu ko? Kawai Kije ki shirya Zan ma Bro magana! Singapore is really fun you'll love it!!" Murmushi Asy tayi sannan ta ce " Ok!" Sannan ta wuce d'akin ta direct ta fad'a bathroom.........

Zaune a Mota ta iske Hydar da Zainab se hira take zazzaga masa tun yana amsawa har yayi shiru se uhm " k'ofar ta bud'e ta shiga sannan ta Mik'awa Hydar wata y'ar takarda , da 'kyar ya karb'a ya duba sannan ya girgiza Kai ya dubi Zainab yace " Zan ajiye ki a wajen su Kim ina da d'an wani aikin da Zan je in na dawo se mu fita "
Fuska Zainab ta had'e sannan ta fice daga motar tana fad'in " Mutum kawai se aiki ya sani ko ni ma bai damu da ni ba " gab !! Ta buga k'ofar motar ta koma cikin gida ,Asy tabi bayanta da kallo baki a sake Maganar Hydar ya dawo da hankalin ta cikin motar " Ai tunda ba drivern ki bane ni se ki dawo gaba ko ?" Murguda baki tayi sannan ta fito ta koma front seat gami da d'aura seatbelt nata ..........

Da gudu ta koma d'aki tana share guntun hawayen ta kamar k'aramar yarinya ta kwanta luf

a cikin luntsumem katifan ta anan har bacci yayi awon gaba da ita.....

Tafiya suke jifa jifa yake shafa sajen fuskar sa yana duba agogon hannun shi , ita kuwa kallon sa kawai take ace wai mutum ko ya batawa wani rai bai damu ba abunda yasa a gaba shi zai yi gashi kuma very grumpy babu dariya kullum fuska a tamke !! Cikin ranta tace " wannan badan he's handsome ba da yanda yake had'a fuskan nan ba ganuwa zai yi ba!!"

Daidai bakin wani ruwa suka tsaya wani jirgin ruwa boat ita suka shiga Asy se dube dube takeyi tana nazarin wajen 'kasa 'kasa tace " Zainab tayi gaskiya! Singapore is amazing!!" Kamar daga sama taji Hydar yace " Idan kika bar wannan tunanin yaci galaba a kan ki zaki wahala kuma ba zakiyi abunda ya kawo ki ba" yana Kai wannan ya shige cikin boat d'in yana gyara zaman rigar shi. Harara ta watsawa k'ofar tace " Ko me ya dameshi da harka ta?"..................

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:10 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🔢🎞️9️⃣5️⃣

Cikin boat d'in kansa abun kallo ne , Asy ta daidaita kanta sannan ta k'arasa ciki, zaune ta iske Hydar ya nad'e k'afa d'aya a kan d'aya se danne danne yake a computer wanda ga dukkan alamu a ciki ya samu don bai shigo da shi ba, waje ta nema ta zauna opposite to him tana kallon Kyakkyawar fuskar shi, mamakin halin shi na ko in kula take yi.....

Hydar kuwa tun shigowarta yaji a jikin shi Ana kallon shi don haka ba tare da ya ce qala ba ya ciro wani bak'in spaces nashi ya kafa a ido yaci gaba da abunda yake yi.... Ganin ya fahimci kallon shi takeyi yasa ta Fara gyaran murya gamida tsuke baki tace "yanzu kuma ena zamu je?"ba tareda ya kalli inda take ba yace JURONG SINGAPORE BIRD PARK

Ido ta juya sannan tace " Do we have a target their? Naga ba address d'in da na baka d'azu ba kenan! " Hydar ya d'ago kai yace " Se kiyi shiru ki ga abunda Zan yi !! For goodness sake Detective I know my work and I decide how I wanna do it!!" Tab'e baki Asy tayi tana kallon shi har ya gama surutan shi sannan ta ciro wayarta tana waya da Azeeza bata ankara ba se gani tayi ya mik'e ya nufi hanyar fita dan haka itama ta d'au purse nata ta bi bayan shi , park ne madaidaici me kyaun gaske tsuntsaye kuwa tabbas akwai iri iri, bai tsaya jiran komai ba ya shige wata bak'ar mota yana jiran Asy , don haushi ji yake kamar yaje ya fisgota don tana b'ata masa lokaci , tana shigowa ya ja motar suka fita daga harabar park d'in.,,,,,,.........

Ganin Hydar ya tsaya jikin wani rufaffen garage yasa Asy ta juyo tana kallon shi , ganin ya ciro bindiga yana sa bullet a ciki Asy ta zaro ido cike da alamar tambaya abunka da me baki tace

"Me kuma zamuyi da bindiga a nan? After all the mission is an undercover mission!" Hydar ko ta kanta bai bi ba yayi ficewar sa yana rufe fuskar sa da hular dake had'e da rigarsa wato hood ganin bashi da niyyar kulata ta Fara bin shi a hankali tana faman lalumar numbern General amma sam bai d'aga ba , Hydar ya dawo da baya ya wafce wayar daga hannun ta ya saka a aljihu ya hankad'a ta jikin bango idon shi cikin nata yace " Young lady behave yourself!! Any slight move here could be noticed!! " Hankade shi tayi itama tace " Toh ba se ayi noticing d'in ba? Haka kawai zaka b'ata min mission! Ni ban san ko Kai waye ba kuma ban san me nufin ka na Hana ni waya ba amma kaji na gayamaka if I smell anything fishy around here kana cikin matsala!"

Tsawa Hydar ya daka Mata " toh se me? Nima ba sanin ki nayi ba kowa kuma da abunda yazo yi nan ! Ni nazo in ga bayan su ke kuma kin zo ki bincike su! Wannan ba shine abunda kike son ji ba!? Toh yanzu kinsan dalilin da yasa nake neman su ! Am to them like a predator!! Ni farauta na fito ba investigation ba , minti ashirin kachal Zan baki ki gama abunda zakiyi ki bar nan ko kuma in had'a harda ke !don duk wanda yayi niyyar shiga tsakanina da abunda nayi niyya shima bazan barshi ba!!!!"

Duk tsoron da ya ratsa Asy bata fasa magana ba " Look who ever you are ni bazan tab'a Bari kayi kisan Kai a nan ba! Se nayi abunda zanyi no matter what!! Do your worst!!!"

" Hmmm Asy ba laifin ki bane!! Rashin sani ne yasa kike min haka but just in case zaki manta later on ina so ki sani kika b'ata min plans nawa you'll face the consequences!!" Tsaki Asy taja tana gyara rolling d'in kanta da gyalen ya warware ta bi ta gefen Hydar ta wuce.............

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:10 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🆖🎞️9️⃣7️⃣

Wani katoton warehouse ta shiga wajen shiru kamar ba'a halicci d'an Adam a wajen ba , a nata zaton babu kowa a ciki hakan yasa ta dinga bud'e bud'e babu abunda idanuwanta ke nuna Mata kamar su cocaine, heroin da sauran muggan makamai , bata daddara ba ta sake bud'e wata y'ar k'ofa ta shiga  babu komai cikin sa se wata kujera a tsakiyar d'akin ita kad'ai se light bulb me Hasken gaske ta sama , kamar daga sama ban ankara ba na hango Detective Asy a sume , wani sangami ya ja ta kamar wata shara ya daurata a kan kujerar sannan ya d'aure da cello tape duk hannayenta ya had'a da hannun kujeran ya d'aure haka bakin ta ma, ya dad'e yana k'are Mata kallo kafin daga bisani ya d'ebo ruwan sanyi a bucket ya watsa Mata ,cikin firgici ta bud'e idanuwan ta , mayafin ta ya dawo kafad'ar ta tsabar galeji gashi babu hanyar yin self defense tunda a d'aure take.

Matsawa kusa da ita mutumin yayi yace " Kyakkyawar fuska! Amma kuma zuciyar cike da kuruciya! Kinga Yammata da nine ke da tun daga k'ofar fari Zan juya na Kama gaba na , amma tsabar rigima da shishigi kika cije kika shigo nan! " Yana magana yana zazzaga purse nata a k'asa Kwatsam ID card nata ya fad'o kallon kallo kawai suke yi shi da ita wata mahaukaciyar dariya ya kufce masa yace " Jami'ar y'an sanda! Detective Asy Khaleel! Ashe kice da biyu kika zo nan! Kin zo neman bayanai ne akan MK ko kuma DON BK ?? Toh Bari na baki wani d'an labari mana! Don BK baya Nahiyar ASIA baki d'aya yana Chan Nigeria ! Haka ma akwai wani sabon labari MK ma yana nan zuwa Singapore nan da anjima kad'an !! Amma zazzafan labarin shine yau zaki Mutu mushe babu kuma wanda zai sake jin labarin ki ! A kan gawar ki Mk zai sha barasa!!!! " menene kalaman ki na k'arshe???! Iye fad'a min mana chika !! Ya ko kin ji tsoro ne!!!""??

Duk wad'annan maganganu da yake yi Asy idanuwanta gam a rufe se zufa take yi kamar daga sama suka jiyo harbi Tas!!" Asy tana d'aga Kai se gani tayi sangamin nan ya zube a k'asa se kurma ihu yake yi , lokaci guda duk ya fita hayyacin sa , Asy dake zaune a kujerar se girgiza Kai take kamar me son cewa "No"! Amma ina Hydar ya sake one step ya tsugunna gaban sangamin yace " David!! Tell me yaushe zai shigo!!?" Kai David ya girgiza cikin rad'ad'in ciwo hak'oran sa duk Jini yace " Over my dead body!!!" Wani shu'umin murmushi Hydar ya saka yace " Don't be so stubborn David I know you wanted to live badly! Kana son rayuwar ka sosai , chance na baka to live , abu d'aya nake so ka sani koda MK yazo in yaji labarin ka yi sakaci har an zo an yi lek'en sirrin ku toh lallai fa kashe ka zai yi its better ka gaya min ko Zan taimaka in barka da rai!! Ko ba komai kaga zaka rayu zuwa lokacin da M.K zai shigo gari!!"

Kai David ya girgiza yace " Bazan sanar da kai komai ba kamun duk abunda kaga dama amma bazan fad'a ba!!" Kai Hydar ya girgiza fuskar shi d'auke da bacin rai a take ya fitar da wata revolver pistol ya d'aura a gaban goshin David Asy tana ta girgiza kai amma ina aikin gama ya riga ya gama! Hydar ya harbe David har lahira a take Asy ta d'auke wuta a wajen kwakwaran motsi ma ya gagareta ta zaro idanuwa waje numfashin ta ko k'arasawa ciki baya yi idanuwan ta kuwa suka kafe a kan gawar David dake kwance cikin jini............

Mik'ewa Hydar yayi ya mayar da bindigan sa cikin Aljihu sannan ya nufi inda Asy take ya sa hannu ya warware Mata cello tape d'in ya cire na bakin ta ma yayi ficewar sa, A hankali take tafiya gyalen na rataye a wuyan ta sam ta kasa magana! Cikin motar da Hydar ya shiga itama ta shige ya fisgi motar bai zame ko ina ba se bakin bird park yayi parking sannan suka fita sukayi bakin ruwa a inda sukabar boat d'in nan suka sameta , Asy ko zama bata yi ba hasalima a gaban boat d'in ta tsaya ta k'urawa ruwan ido bata ma san sun iso ba seda driver ya Mata magana , Hydar kam tuni har ya isa wajen motarsa ko ta kanta bai bi ba balle ma yasan me take yi!

Babu kofa a cikin falon , Uncle Junaid ya fita don haka Hydar ya ajiye wayoyin sa ya juya ya nufi hanyar d'akin sa, wani zuciya ne ya tahowa Asy a fusace tabi bayan sa , tana shiga d'akin ta hankad'a shi saida ya dafe hannun shi a center table d'in d'akin tukunna ya d'ago jajayen

idanuwan shi yana kallon ta.

" Who the hell are you?! Tambayan ka nake Hydar! Kai waye! How dare you kill David! Haka ake investigation! ? Malam kaga ni ban san kai waye ba kawai an turo ni akan zaka iya taimaka min a kan investigation d'ina amma by the look of it you are nothing but a bloody murderer !!! Kai baka d'auki ran mutane a kan komai ba , kai dakiki ne ! Shin baka sani ba ? Ta iya yiwuwa yana da Mata harda y'ay'a yaya kake zaton zasu ji idan har ta rasa mijin ta ko kuma suka rasa mahaifi?!!"

Hydar da ya riga ya gama fusata musamman da tace masa shi dakiki ne bai san lokacin da ya hankad'a ta ta bugu da bango ba cikin tsawa yace " Idan kuma hakan ta faru da yarinya y'ar shekara biyar fa? Da yaro d'an shekara sha d'aya! ? Ina nufin idan aka kashe musu iyayen su babu tausayi babu imani a gaban idon su , yayinda uwar ke d'auke da k'aramin ciki! Shin yaya kike tsammani rayuwar su zata kasance?! Asy shin kin tab'a rasa wani daga cikin y'an uwanki ? Kin tab'a fuskantar irin cin fuskar da na fuskanta a rayuwa? Da kin san waye MK da wallahy duk abunda Zan aikata bazaki ko d'aga kai ba! Naji ni dakiki ne! Amma ina so ki sani babu wani mahalukin da ya isa ya shiga tsakani na da wad'annan azzaluman se naga bayansu d'aya bayan d'aya se sannan ne tukunna zan iya sauraran kalaman ki  yanzu koda zaki mutu bazaki chanza ni ba Asy! Saboda haka idan kin ga dama ki koma Chan Newyork inda kika fi wayo ki barni nan! I was born to destroy Mk se na sa ya d'and'ana azabar da suka d'and'ana shekaru sha biyar  da suka wuce ! If you like call me names Asy but ina so ki sani I AM NONE STOP!!!! "

Da gudu Zainab ta rungume yayanta tana kuka tana fad'in " Yaya kar ka barsu da rai ka harbesu duk! Badan su ba da yanzu ina tare da Mommy , dalilin shi na rasa kowa ,kai kad'ai ka rage min yaya kar ka Bari suci galaba a kanka ! Kada ka kyale su yaya! Kada ka kyale su!!

Rungume ta yayi yana shafa gashin kanta , Asy dake tsaye duk sun dulmiyar da ita a duhu ta kasa fahimtar me yake faruwa gaba d'aya ta juya da sauri ta fice daga d'akin ta nufi d'akin ta gamida zubewa a kan gado..............

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:10 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
9️⃣7️⃣🎞️1️⃣0️⃣0️⃣

" Dad! Nifa wannan mutumin da ka had'a ni aiki da shi yana matuk'ar bani tsoro! Ban san waye shi ba but meyasa bashida tausayi bai damu da damuwar da wasu zasu shiga ba? Ka duba fa d'azu ya kashe mutumin da zai bamu clue about MK amma ko a jikin sa and he have the guts to shout at me wani wai ""I am non stop""!!! He's very dangerous! "

General yayi gyaran murya yana murmushi yace " My dear ki 'kara hak'uri kuma duk abunda yayi ki bishi a hakan , he knows what he's doing!" Asy ta marairaice tace " Haba Dad waye shi da zai dinga yin abu son ransa ? Who d hell is he??" Daga bayan ta tajiyo Murya yana fad'in

" N.F.S !! Nigerian force services! An undercover agent LIEUTENANT GENERAL HYDAR ALIYU ABDOUL-RAHMAN!!!! "" juyawa Asy tayi cikinta ya dura ruwa tana d'aga kai sukayi ido hud'u da Hydar tsaye bakin k'ofa fuskar nan tamke babu alamar fara'a tattare da ita , k'arasowa yayi cikin d'akin ya wuce ta ya nufi wajen wani shelf dake d'akin ya ciro files guda biyu ya bi gefenta ya fice abunsa , a hankali ta Fara mayar da wayar nata kan kunnen ta cikin murya me rawa tace " Dddad.,., da gaske ne abunda ya fad'a?" Murmushi General yayi yace " My daughter! Abubuwa da dama sun faru a rayuwa! Duk yanayin da kika ga mutum kar ki raina hakan rayuwar Hydar cike take da bakin ciki ki bishi yanda yake so , bai fiye son shishigi ba , Anjima zamuyi magana !!"

Jiki a sanyaye ta ajiye wayar tana tuna kalaman da ta fad'a masa tace " Lallai yau na kwafsa! Lieu gen Hydar na k'ira dakiki??" Bata kammala tunanin da take ba wayar ta sake 'kara, Wannan Karon abokin aikinta ne Jones dake Newyork nan suka d'an tab'a hira Azeeza na gefe tana jin su Jones ya sanar da ita zasu zo Singapore tare da Azeeza don kammala binciken kisan da suke yi saboda haka ta nema musu waje! Bayan Ta ajiye wayar ne yayi daidai da shigowan Uncle junaid ta zata maganar Hydar yazo yi amma to her surprise se yace " Ki sauk'o muci abinci " Kai kawai ta girgiza masa shima ya juya , Har zai fita kuma se ya juyo " You look disturbed Asy! Akwai wata matsala ne?" Murmushi tayi sannan ta sanar dashi cewa Su Jones zasu zo ko zai taimaka ya basu masauk'i murmushi ya Mata yace " its ok akwai enough space , ba komai Allah ya kawo su lpya , Ameen ta amsa tare da bin bayan sa suka nufi dining d'in.............

Sauk'owa yake yana Danna wayarsa kanshi a k'asa har ya iso dining area d'in ba tare da ya d'aga kai ba yaja kujera se sannan ya ajiye wayar ya d'ago yana kallon Zainab da take ta fama da pasta gasu dogi , dariya sosai ya Fara yana kallon ta itama ta d'ago tana masa dariya , ya tuna tun tana k'arama tana son abun amma kafin ta cinye se bakinta ya gaji don tsayin pastan , seda ta gama had'iye wa sannan ta d'auki fork kamar zata choke shi ,da sauri ya matsa yana fad'in " Dole ne se kin ci? Nan gaba bakinki se yayi tsayi! Ummmm kiyi ki gama mu fita cikin gari ,ina son zuwa shopping " ya k'are maganar yana jefa peanut a baki , kallon sa kawai Asy take yi kafin ta mik'e zata koma d'aki da sauri Zainab tace " Sis! Baza ki bi mu bane ? " da sauri Hydar ya mik'e ya ce " Ke Zee ! Ki kyale ta mana Ana dole ne? Tunda kika ga ta tashi bata da niyya ni bana son shishigi" baki zainab ta turo tace " toh kuma yaya .........." Bata k'arasa ba yace " Shhhhh ki gama zukar pastan ki mu tafi kar ki min wasting time! Next week zamu koma Nigeria" tsalle sosai Zainab take tana buga k'afa wai ita sam bazata koma Nigeria ba , shi kuwa kawai ya tsaya yana kallonta yana mamaki at the same time abun ya mugun bashi dariya ,kamar bai ganta ba yayi yaci gaba da jefa peanut a bakin sa yana Danna wayarsa , Chan da ta gaji ta matso kusa dashi a hankali tana kallon abunda yake yi a waya kafin tace " Yaya wai kai baka cin abinci ne? Bai ko kulata ba ta sake matsowa tace yaya bani wayanka nima Zan buga game d'in da kake yi " Nan ma bai ce Mata 'kala ba ganin bashi da niyyar magana ta wafce

wayar ta ruga a guje shima ya bi bayanta yana kiranta amma ina tak'i tsayawa ta fice Daga falon suka fita filin gidan daga gefe ruwa ne yake zuba ga dukkan alamu bayi ake wa grass d'in wajen da flowers ,nan ta d'auke hose (Tiyo) d'in ta yi pointing a setin Hydar duk ta jik'e shi jagaf da ruwa ,Asy tana saman balcony tana Kallonsu with adoration , she really missed her brother😘

Jefar da hose d'in tayi ta nufi inda suke parking motoci tana fad'in come on yaya! Catch me if you can!!!! Girgiza kai yayi sannan ya nufi inda take , Out of nowhere yaji ya ci Karo da abu , tun daga k'asa har sama yake kallon ta , pencil jeans trouser ne jikin ta se blue kaftan top da ya wuce cinya da kad'an se kuma farin mayafi data yafa ba tare da tayi rolling ba , handbag nata Sak jeans d'in jikinta ,takalman ta ma blue ne, kallon sa ya mayar zuwa kan fuskar ta wani abun mamaki Sak take Kama da Zainab d'in sa Banbancin su tafi Maryam girman jiki kuma tana da bulin hanci wanda ta saka masa stone fari me kyau.........

Murmushi ta sakar masa tace " Am sorry ! Am by name Azeeza MK An FBI agent Mujhe Detective Asy Khaleel se Milne ayee"(I have come to meet detective Asy) a zaton ta Hydar indian ne 😂

Ba tare da ya kalli inda take ba yana matse ruwan rigar shi yace " Asy khaleel tana ciki "amsar sa kenan a tak'aice , zaro idanuwa tayi waje tace " Oops sorry ! Nayi zaton kai d'an nan ne , tare muke da abokin aiki na I hope ba matsala in ya shigo?" Nan ma bai kalleta ba ya juya yana fad'in " In kinga dama !" K'ugun ta tarike tace * Lallai ma wannan mutumin shi me ya d'auki kansa ne???"

Hydar yana shiga falo ya duba bai ga Uncle Junaid ba da sauri ya haura side nashi ,tsaye ya iske shi yana gyara rigar sa ga dukkan alamu fita zai yi , a hankali ya juyo yace "Yaya dai Soldier? " yana maganan yana neman wajen zama.

Hydar ya nisa sannan yace " Yar gidan MK ! Itace Uncle! Itace abokiyar Aikin Asy Khaleel uncle idan har na barta a nan wataran Zan iya cutar da ita!! Kace ta fita! Kaje kace ta bar min gida!!!" ..........,,,,.......

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:10 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🔟1️⃣🎞️1️⃣0️⃣5️⃣

Uncle Junaid ya dube shi cike da nazarin yanayin da Hydar d'in ya shiga, sannan yace " Soldier!! Ya kamata ka kwantar da hankalin ka! Ta yiwu ma bata san komai ba kai dai concentrate akan abunda kake yi kawai!" Kai Hydar ya girgiza yace " No! No uncle bazan iya ba! Kawai ta fita !! Yanzunnan zan samu Asy she has to leave ko kuma in fitar da ita da kaina!"

Da sauri uncle Junaid yasha gaban shi yana fad'in " Kana d'aukan wani slight chance na korar ta to lallai zata gane Kaine d'an uwanta Hydar kuma tabbas zata sanar da MK cewar ta samu d'an uwanta kaga nikam akwai possibility zata gane ni bazan ma bayyana fuska na a gareta ba! Amma kai kam da ta riga ta had'u da kai kawai kayi kamar baka san tana yi ba domin in ta gane d'an uwanta ne kai lallai zata sanar da MK kana raye , yanzu de ba wannan ba! Na samu labarin cewa MK zai shigo yau! Akwai possibility zata had'u da shi domin na tabbatar tasan da zuwan sa Singapore saboda haka ka zuba Mata ido!!"

Hydar bai ce komai ba ya juya ya fice Uncle junaid yayi Murmushi yacigaba da abunda yake yi . A falo ya iske Zainab ta shirya tsaf cikin doguwar riga brown ta yafa mayafin ta tana ta wasa da wayar Hydar , sand'a yayi ta bayan ta ya wafce wayar sannan yayi tsalle ya hau kujerar yace " Finally! Yana nuna Mata wayar, kusa dashi ta dawo tana zumbure zumbure , kallon ta kawai yake yi yana Murmushi yace " Ki tashi mu tafi shopping d'in" daga bayan su suka jiyo Murya tace " Wow! Shopping? Can I come with you guys?" Dariya sosai Zainab tayi tace " Aha! Kaga Mun samu Karin company!" Hydar ya had'e rai yace " waye kuma wancan?" Zainab ta ce "Haba de yaya! Baka ganta bane d'azu ai bakuwar Asy ce dazu suka zo da wani bature Jones wlhy suna da ban dariya! Yaya muje da su pls ! Pls! Pls yaya!"

Tab'e baki Azeeza tayi tace " dubi yanda ya tsare ya nuna bai sanni ba bayan dashi muka Fara had'uwa cikin gidan! " ba tare da ya Saki fuska ba yace " se ku fito ai ni ina sauri ne! " Hydar bai yi hakan dan son ransa ba yayi ne kawai don baya son ya sake batawa kanwar sa rai kamar yanda yayi d'azu da safe.

A gaban motar Jones yake Hydar na jan su  Zainab Asy da Azeeza kuwa suna baya Duk surutan da Suke yi Hydar bai ce ko A ba hasalima kunnen shi rufe yake da earpiece , babban shopping Mal dake North East Hougang mall suka shiga , seda Hydar ya tabbatar kayatattun kayayyakin ciki ya d'ebe musu hankali yace ma Zainab zai d'an ga wajen in sun gama shopping su k'ira shi sannan ya mik'a Mata credit card nashi ya fice.

Asy ta Lura da fitar shi don haka tabi bayan shi ,taxi ta tare sannan ta nuna mishi motar Hydar ba musu ya Fara bin bayan Hydar.........

🖊️ Bayan tafiyar su Hydar daga warehouse da awa d'aya MK ya shigo Singapore, tun daga hanya yake k'iran David amma shiru duk da haka bai daddara ba saboda yana da Appointment , Isar su ware house d'in suka iske Gawar David MK ya sa su bincika duk gurin for anything suspicious anan ne suka iske ID card d'in Asy Khaleel😳 MK ya karb'a yana Murmushi ya kalli mutanen sa yace " Find the girl!!!"

A lokacin suka bazama neman Asy cikin Singapore!!!!

Jeeddah jao🏵️
[10/20, 10:11 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🔟6️⃣🎞️1️⃣1️⃣0️⃣

Hydar yana parking motar shi ya nufi wani  building me tsayin gaske Asy bata daddara ba ta bi bayan sa har zuwa floor d'in da ya tsaya , wani d'aki ya shiga gami da barin k'ofar half opened Asy tana isowa ta rakab'e bata ankara ba taji an Fisgo hannunta har cikin d'akin gami da rufe k'ofar. Husky voice nashi tajiyo yana fad'in " Mesa kike bina? Are you out of ur senses? Ni d'in ma investigating nawa zakiyi ko kuma me?"

Murya na rawa Asy tace " I was just trying to help" . wani murmushin bacin rai yayi yace " Help?  Help who? Kafin ki yi tunanin taimako na me zai Hana ki Fara taimaka wa kanki?" Zaro idanuwa Asy tayi ta aza su a kan na Hydar sannan tace " Ni kuma? I don't understand" tsaki yaja gami da Kama kunkumi ya doki wata kujera cikin bacin rai yace " How comes kika jefar da ID card naki a warehouse? Yanzu gashi MK ya iso and his men are hunting for you! You are now his prep and believe me idan ya Kama ki kashe ki kawai zai yi .      Kallon cikin idanuwan shi Asy take yi kafin tace " Waye MK? Meyasa ka damu da kaga ka ga bayan shi? Yanda ka damu hakanan yasa na kasa samun nutsuwa domin dole se akwai kwakwaran dalili? Haka ma wancan ranan naji Zainab na kuka tana fad'in ka kashe shi! Me yasa? Me ya faru da ku dalilin MK iye??"

Ajiyar zuciya Hydar ya sauk'e ya juya gami da rufe idanuwan sa sannan ya Fara bata labarin MK , duk abunda ya faru seda ya sanar da ita Asy tayi kuka sosai ta tausaya musu , se taji ta kasa samun sukuni. Hydar kuwa kallon ta yake yana kafin yace " Wai in tambaye ki mana? "

D'agowa tayi tana kallon sa tace " Allah yasa na sani". Hydar ya zauna kusa da ita yana mai kallon ta yace " Me yasa ku Mata kuka cika saurin kuka? I mean everything simply get you emotional ?" Murmushi Asy tayi tace " Wannan shi ake Kira da mace! Haka muke bama iya 'boye duk wani feeling namu unlike you men! Especially brave ones like you koda kunga abun tausayi zuciyar ku is strong sedai idanuwan ku su nuna! Mu kuwa hawayen mu shine symbol na emotionality a wajen mu and that is what differentiate mace da namiji."

Tab'e baki Hydar yayi yana kallon ta yace " kenan idan da kece in my place fifteen years back da kin dad'e da mutuwa kenan?" Kai Asy ta girgiza tace "Of course yes!! " Dariya Hydar yayi wanda ya fitar da fararen hak'oran sa yace " gaskiya indai haka ne baki chanchanci zama detective ba kyaunta kawai ki koma gida ki makala apron ki d'auki tukunya ki hau girki!" Yana maganar ne yana mai kashe Mata idanu " dariya sosai ya bata tace " babbar magana Malam! " Murmushi ya Mata sannan yace " Me Azeeza ta zo yi  a Singapore?" Kallon shi tayi tana mamakin tambayar nashi tace " Tazo aiki ne , akwai wani murder case da ake yi ne da case d'in a hannu na yake da na taho aka damk'a Mata case d'in so tazo neman wani clue ne a nan, Amma mesa ka tambaya??"

"Azeeza Mk y'ar gidan MK ne , mutumin da muke nema! She's a sister to me! Bata sani ba

ne , I believe tasan inda MK yake ina so in san duk wani motsi nata!!" Hydar ne yayi maganar idon shi cikin na Asy sannan ya mik'e yana kallon window , hannu yasa a hankali ya d'aga labulen a wajen ya hango mutanen MK suna shigowa building d'in da sauri ya juyo yana kallon Asy yace " Perfect! Mutanen Mk sun iso I know you are a player so play well Baby!" Asy tayi murmushi sannan tace " Amma gaskiya Kazo da wuri don ka riga ka saka min tsoron MK a raina! Idan na shiga hannun su baka iso in tym ba they might hurt me! " Kai Hydar ya girgiza mata yace " na saka tracking device a jikin zoben nan gashi ki saka , duk inda kuke Zan gani kuma Zan ji me suke fad'a miki don haka se ki dinga sanar da ni tsarin wajen cikin fasaha I'll be right behind you!" Kai Asy ta girgiza ta amshi zoben ta saka a ya yatsan ta sannan ta bud'e k'ofar ta fice ,se addua take yi Allah ya bata nasara!"

Wani daga cikin mutanen ne ya yi shouting out sauran ma suka nufo inda yake ya Fara nuna musu Asy , ganin haka yasa Asy ta ranci ta kare🏃🏃 suma suka bi bayan ta , bata wani basu wahala ba ta tsaya suka chafke ta gami da. Tura ta cikin motar , d'aya daga cikin Mutanen bai shiga motar ba yace da su su k'arasa shi zai duba wasu clues hakan yasa suka tafi shi kuma ya koma cikin building d'in ,d'akin da Hydar yake ya shiga gami da cire mask d'in fuskar shi . Murmushi sosai Hydar yayi yace " My man! Aikin ka yana kyau pls kar ka Bari su cutar da ita ,and I hope ka kawo min address d'in? " Kai mutumin ya girgiza sannan ya mika wa Hydar paper d'auke da adreshin inda MK yake , Hydar ya yi shiru sannan yace

" Make sure basu cutar da Asy ba! Domin if anything happens kafin na iso toh lallai kowa zai kuka da kansa , aikin ku yana kyau ! Yanzu nasan zai tambayi Asy dalilin kashe David kada ku yadda tayi linking kisan da kanta ina so ku sanar da ita ta fad'a masa cewa Ajalin sa ne yayi kisan ALIYU ABDOUL-RAHMAN ( MAHAIFIN HYDAR )!!!!"

wannan zai girgiza shi ainun da 'kafar sa zai nemi ya koma Nigeria kafin nan Yau Zan gama da mutanen sa! So stay alarted!!!!" Kai mutumin ya girgiza ya juya ya fice yabar Hydar a d'akin zaune yan duba laptop d'in shi ,,,,,....................

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:11 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🎞️1️⃣1️⃣5️⃣

" Detective Asy Khaleel!!! Sunana MUHAMMAD KABEER ABDOUL-RAHMAN (M.K) Gaskiya naji dad'in had'uwa dake !!!" Wani shu'umin murmushi Asy tayi a galabaice tace "Ni kuma naji haushin Had'uwa da kai!!"

MK yayi dariya " Hahahahahahhh! Alamu sun nuna ! Kina jin haushin MK sosai!!" Asy ta

harare shi sannan Tace " Daga yara har tsofi kowanne yana jin Haushin MK wannan shine gaskiyar magana!" MK yayi dariya harda rik'e ciki yace " Babbar magana ! Ga dukkan alamu kema na tab'a rayuwar ki kenan!?" Ba wannan ba ma ena HYDAR?😳

Duk da cikin Asy ya dura ruwa bata san lokacin da ta dake tace " Ohhhhh! Na manta da jakata a gida ba mamaki yana ciki!!"  Dariya duk mutanen wajen suka Fara shima MK ya murmusa yace " Aikin ki aiki ne na bincike ! Na fiki sanin aikin ki Agent Asy Khaleel! Nasan ba ke kika kashe David ba! Saboda ke mace ce? Toh me zai Hana ki. Had'a ni da shi zakin in yaso se kija gefe ? Matsalar mu da Hydar daban ce! Kija gefe ko zaki rayu cikin salama!"

Wani mugun dariya Asy tayi tana fitar da numfashi da kyar tace " Ina tausaya maka MK!!" Shima dariya ya Mata yace " da Alama ke masoyiyar Hydar ce?" Kallon shi tayi ta gefen ido tace " Masoyiya? Ai na ma fi k'arfin hakan!  Zuciyar Hydar TANA TARE DA NI (littafin miemiebee)  da ita nake rayuwa! Idan baka sani ba ka sani!!"

MK yace " What!?!! Gaba d'aya kekam mahaukaciya ce! " dariya sosai Asy tayi tace " Kaima ai haka nake gani a kanka! " dafe goshin sa yayi yaja kujera ya zauna yana facing nata yace " ki min abu d'aya mana! Ki zama yarinyar kirki mana! Ki fad'a min waye Hydar yake hari a cikin yara na?? Yawu Asy ta tofa ma MK a fuska tace " Ai ko zaka kashe ni bazaka ji wannan daga baki na ba!!"

Hydar yana mota yana jin duk abunda ke faruwa , d'ago kan shi da zai yi ya hango wata mota ta tsaya Chan nesa da nashi , wata budurwa ce ta fito fuskar ta toshe da gilashi bak'i Tasha bak'ak'en kaya riga da wando , wasu mutane uku ne bayanta da alama bodyguard's nata ne duk da a nesa take hakan bai Hana Hydar ya gane ko waye ba "AZEEZA!!!? ya tambayi kanshi da kanshi sannan yace " Kenan ta san ko shi waye? Ita ne kenan ta fad'awa MK cewa shine? Yana cikin wannan tunanin wayar sa tayi 'kara

Yana d'aga wayan uncle Junaid yace " Hydar ! That Azeeza is a crook! Naji maganganun ta a waya da MK! Tasan komai hasalima ita ta sanar da shi plans naka! " Hydar ya bugi motar sa yace " Amma Uncle wa ya fad'a Mata plans d'in?" Uncle junaid yayi ajiyar zuciya yace " Yanzu haka ina asibiti da Zainab! She drugged her! Magani ta bata wanda ya bugar da ita don haka ta fad'a Mata komai , yanzu haka Azeeza bata nan! Ta fita ban kuma san ina tayi ba but we have to stop her!!!"

Hydar yace " Uncle yanzu na ganta ta shiga wajen MK amma ina son in ga zainab am scared kar wani abu ya sameta! " uncle junaid ya girgiza kai " No Hydar ! Komai zai rushe idan ka zubar da plans d'in ka , nasan Allah yana tare da mu don haka stick to ur plans , yanzu Zan yi magana da general " Amma ban san yadda Zan yi ba saboda Asy y'ar gidan General ne!"

Zaro idanuwa Hydar yayi yace " Yar gidan General? Kenan General y'arsa ya turo min muyi

aiki tare? Why would he make this decision? " uncle junaid yace " Hydar yayi hakan ne domin bai yarda da kowa ba don haka yanzu ne lokacin da zaka nunawa general cewa you are greatful for halaccin da. Yayi maka a rayuwa!!"

Hydar bai tsaya bata lokaci ba ya fita daga motar yana gyara zaman bindigan shi ta cikin rigar shi sannan ya bud'e Wani k'ofa underground ya shiga................

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:11 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🔟🎞️1️⃣2️⃣0️⃣

Uncle junaid ya rik'e wayar yana k'iran sunan Hydar " Hydar ! Hydar !! Don't you dare get in there alone ! Kar ka shiga kai kad'ai !!" Shirun da yaji ne ya tabbatar masa Hydar baya kan wayar da sauri yayi dialing wata number , ( Nima kaina Jeeddah ban tsaya jin me zai fad'a a wayar ba na koma wajen Hydar don ganin yadda zata kaya 😅).....

Tafiya yake agogon hannun sa yana blinking green light, daidai wata k'ofa blink d'in ya karu this tym around Jan signal ne Hydar bai tsaya wata wata ba ya murd'a hannun k'ofar ,a bayan wani k'aton shelf na takardu ya tsinci kansa daga nan yana iya jin maganganun MK don haka yayi sand'a ya doshi jikin shelf d'in ya zare wasu files hakan ya bashi ikon ganin bayan Asy Khaleel kuma yana kallon MK , A hankali Azeeza take zagayo wa ta bayan Asy wata y'ar wuk'a ta mik'a wa Asy secretly ta bayan hannu

Duk wannan abun Hydar yana gani, A ransa yace " Me Azeeza take nufi? Meyasa ta bawa Asy wuk'a? Kenan itama so take tayi tracking baban nata? Toh amma me yasa ta so jin plans d'ina a wajen Zainab ? Ganin bashi da amsar tambayoyin nasa yasa Hydar ya mayar da duban sa ga hannun Asy yana ganin yadda take kokawar yanke d'aurin da suka Mata ,
Azeeza ta fita tare da mutanen MK tana gaba suna biye da ita ,d'akin ya rage daga MK se Asy
Cikin tsawa MK yace " Am asking you for the last time ena Hydar yake?" Asy ta bushe da dariya tace " Hydar ko Aliyu? Ka manta ne? D'an uwanka? Lt col Aliyu Abdoul-Rahman ? Ka manta ? " MK ya Kama kan shi da hannu biyu yace " Ke ! Ke! Ke!!!! Ya ishe ki haka!!! Zan kashe ki! Zan kashe ki!!" Dariya Asy tayi tace " Ai kaikam taka ta k'are mutuwar ka na gaban ka! Ina so in san kalaman ka na k'arshe!!!"

Duka ya kaiwa Asy wanda yasa ta Saki 'kara bai ankara ba yaji an shak'e wuyan shi d'agowa yayi da kyar murya ciki ciki yace " WWHOO AARRRE YOU!!"

dariya Ya kufce wa Asy tace " Ji yanda yake burga d'azu yana fad'in wai ena Zaki na amma yanzu da zakin ya kawo kanshi gaba d'aya ya fita hayyacin shi! Shi ban gaya maka ba MK ?

Nice na shiga tsakanin ka da mutuwar ka , amma yanzu da mutuwar taka ta iso dole na matsa na baka guri , jibi yanda kake zare idanuwa kamar ba Kaine kake Kurari d'azu ba?" Tana kai wannan ta fice daga d'akin tana dariya ya rage daga Hydar se MK.

" Me suka maka? Me suka maka zaka kashe su? Shi ya d'au nauyin karatun ka! Ya inganta maka rayuwa , daidai da Rana d'aya tun da na taso ban tab'a ganin ya b'ata maka rai ba! Ita kuma Mommy laifin me tay maka?wawa butulu! Mara imani mara mutunci! "

A fusace Hydar yake maganar har numfashin sa na daukewa jikinsa na rawa ya rasa yanda zaiyi , kafafun sa da suka kasa d'aukar sa ya rik'e sannan ya ja kujera ya zauna! Yace " Da ace ni butulu ne irin ka da a gaban y'ar ka zan kashe ka kamar yadda ka kashe iyayena a gaba na! But you know what? That is what differentiate Tsakani na da kai! "

" Hydar dan Allah ka min rai! Sharrin shaidan ne wallahy ,da rud'in duniya! Kamun afwa" Hydar yayi wani murmushin takaici yace " Lokacin da zaka kashe su basu rok'eka cewar kayi hak'uri ba? Shin ka hak'ura ne? Ka fad'a min ena zan samu Don BK???" MK ya zaro idanuwa yace " Don BK kuma? Ni ban san shi ba!"

Hydar ya ciro bindigan shi ya harbi k'afan MK wanda hakan yasa ya Saki 'kara na azabal! Hydar ya dubeshi yace " Don BK nace maka! Ena yake ? Mk yayi dariyar azaba yace " ko na fad'a maka ko ban fad'a maka ba kashe ni zakayi toh saboda haka bazan fad'a ba !! " Hydar ya mik'e yana kallon yatsun hannun sa sannan ya juya baya yana murmushi ba tare da ya waiga ba ya dinga sake harsashi a jikin Mk zuciyar shi ta bushe baya ji kawai harbi yake , da gudu Uncle Junaid ,Asy da Azeeza suka shigo ciki Junaid ya Hankade Hydar a k'asa sannan ya wafce bindigan Hydar ya rufe idanuwan shi ba tare da ya tashi ba daga k'asa.

Azeeza ta zube kan gwiwar ta tana hawaye Asy kuwa ta kasa koda motsi , tabbas taji tausayin Azeeza amma ba yadda ta iya MK has to face this , in fact he deserves more than that!............

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:11 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🎞️1️⃣2️⃣5️⃣

A hankali Hydar ya zauna gami da nad'e kafafuwan sa kamar me shirin cin abinci , Azeeza ta taso ta fad'a jikin shi tana kuka me ban tausayi " Yaya dan Allah na rok'eka pls kada abunda Abba na ya aikata ya zama silar saka k'iyayyar ka a gareni! Banda kowa ku kad'ai kuka rage min , tun ina y'ar shekaru takwas na Fara kewar ku , na rabu da ku ba tare da son raina ba! Daddy yaso cusa min tsanar ku a raina ganin bazan d'auka ba yasa nayi nesa Daku! Yaya pls don't ignore this lone sister of urs "

Hydar bai ce komai ba se shafa gashin kanta da yayi sannan ya maida duban sa gareta yace " Am sorry! Am sorry!!" Azeeza ta d'ago jajayen idanuwan ta tace " Don't be ! He deserve this , yaci amanar yanuwantaka sannan ya ci amanar k'asa baya buk'atar duk wani Mercy ! "

Wayar uncle junaid ne yayi 'kara a take ya Mik'awa Hydar. Ba tare da yace komai ba General yace " Finally! MK is down! Na samu whereabouts na don BK , yana nan Nigeria kuma muddin yaji Mutuwar MK zai girgiza ko yayi k'ok'arin barin k'asar don haka dole wani yayi basaja a matsayin MK kafin ka gama shirye shiryen ka na dawowa Nigeria, Soldier kana ji na kuwa?"

Se lokacin Hydar ya Saki ajiyar zuciya yace " Yes sir."
Bai jira wata maganar ba ya mik'a wayar wa uncle junaid sannan ya janye daga jikin Azeeza ya fice daga d'akin suka bi bayan shi , uncle junaid yana k'iran shi " Soldier!! Ena kuma zaka je?" Ba tare da ya juyo ba yace " Autar Hajiya Zan duba asibiti Zan je kar ta tashi ba kowa kusa da ita " duk da ma Junaid ya bar Detective Jones a kusa da ita bai Hana Hydar ba saboda yasan bai isa Hana shi ba......

Uncle junaid ne yasa aka wuce da gawar MK fridge dan preserving sannan suka wuce direct gida , mutanen da Azeeza ta fita da su kuwa tayi handling nasu a hannun strict security na k'asar Singapore ................

Jeeddah ja'o🏵️
[10/20, 10:11 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🔢🎞️1️⃣3️⃣0️⃣

Asy, Uncle Junaid da Azeeza ne suka shigo asibitin ,to their surprise basu iske Hydar ba, hasalima Zainab tace bai zo Asibitin ba . Sau tari junaid yana k'iran wayar sa amma sam bata shiga kuma sun kasa tracking inda yake, hankalin su ya tashi musamman ma Asy Zainab ma mamakin damuwar tayi , Azeeza kuwa kallon ta kawai take yi cike da mamakin yadda ta damu! Cikin ranta tace " Irin damuwa haka? Does it mean she has a feeling for yaya?"

Hydar na hango tsaye a bakin ruwa kanshi da face cap bak'in T-shirt riga ne jikin shi da blue jean hannun rigar ta matse hakan ya bayyana k'aton damtsen shi , waya yake hankali a kwance kamar babu abunda yake yi seda yakai minti biyar yana dube dube sannan ya ciro waya daga aljihun sa yana dannawa yana karawa a kunne naji yace " Ina bakin ruwa kusa da MARINA BAY SAND INTEGRATED RESORT " daga nan ya katse wayar ya nemi waje ya zauna yana kallon yanda jirage cike da mutane suke shawagi kan ruwan ya shafe minti goma sha biyar a haka kafin nan wayar ta sake ringing ,wannan Karon da ya d'aga bai yi magana ba se Mik'ewa yayi yana murmushi , wani tafkeken jirgin ruwa wanda zai iya d'aukan mutum d'ari da wani abu ne ya tsaya a gaban shi ,to my surprise se naga duk sojoji ne a kai sun kasa sun

tsare da bindigogi daka gansu kaga mutanen Russia dun ko maganar da suke yi ma yaren Chan ne , ganin ba sanin yaren nayi ba naja gefe na tsaya Hydar yana tafe ina bin bayan shi,

Duk mutanen babu fara'a a fuskar su haka shima lokaci guda Hydar ya murtuk'e fuska ya k'arasa cikin jirgin , wata chika ce ta fito sanye da kayan soji se kwarkwasa take gata kamar zata karye tana masa magana ma ko gefen ta bai kalla ba hakan yasa ta b'ata rai ta bi bayan sa amma kafin ta iso ma ya maida k'ofar ya rufe bam!!! A fuskar ta har seda ta tsorata

Cikin wani operations room ya shiga nan ya tarar da wani dattijo shima shigar sojin ne dashi amma kuma Hausa yake yi " Hydar my Son! Aikin ka na kyau! Finally Ka kawo reign din MK to an end! " Murmushi sosai Hydar yayi yace

" All these wouldn't be possible without you GENERAL ( BABAN ASY KHALEEL😳 ) a hankali naja baya nace " Wai wannan ba shine dazu yace Don BK yana Nigeria ba  toh ya akayi ya zo Singapore kodai duk daman shiri ne"?

General ya mik'e yana girgiza kai " A'a d'ana! Sau nawa Zan fada maka nafi preferring Dad akan general kodai har yanzu ban kai matsayin Lieutenant colonel Aliyu bane?" Sosa 'keya Hydar yayi yace " ka min afuwa Dad! Bazan sake ba ! You are more than a father! Bazan tab'a mantawa da kaiba a rayuwa!" Murmushi General yayi sannan yace " I have a surprise for you!" Hydar yayi murmushi yace " Surprise? I love surprises!" Duk suka bushe da dariya yayin da general ya shige gaba Hydar na biye da shi a baya......

Wani d'aki mai duhu suka shiga general ne ya kunna wutan shi kanshi wutan d'akin jajir yake Hydar ya ga mutum d'aure kan kujera ya sha bugu kamar ba gobe  fuska d'auke da alamar tambaya ya kalli General yace " Dad! Is this what I think it was!? " General ya girgiza kai alamar " Eh"

Hydar ya Saki murmushi yace " Don BK!  What a pleasant surprise! Mutumin nan ya mugun k'warewa a gun iya basaja! Shin ba d'azu kace min BK yana Nigeria ba? " General  yayi murmushi yace " Ai nima bai san cewa babban d'an basaja bane! Wanda ya tura Nigeria mukayi tracking da duplicate MK hakan yasa yayi sakaci ya bayyana wa Duplicate MK cewa Ai Don BK yana nan a Singapore ,Mistake d'in da Don BK yayi kenan da bai gayawa MK din asali cewa yana Singapore ba ,so shi wancan ya b'ata masa plans nasa ya fad'i cewa yana Singapore ni kuma tun last week nabar Nigeria ba tare da na sanar da kai ba don bana son hankalin ka ya rabu biyu saboda haka ne ma na mayar da number na private number don kada ka gano"

Dariya Hydar yayi sannan ya d'aga fuskar Don BK sannan ya sake ya Kama kunkumi yana murmushi wanda ya manta lokacin da yayi irin sa sannan yace " General! Oh I mean Dad! Kasan wani abun mamaki kuwa?"

General ya girgiza kai yace " Um um ! Se ka fad'a Soldier! " murmushi Hydar yayi yace " Don BK ba sunan shi bane ! Koda Mun kashe shi Don BK yana nan! Domin kuwa akwai files da

documents wanda Babana ya yi bincike akan Don BK asali BK d'in sunan wani Nuclear weapon ne da suke aiki a kai shi kuma wannan shine Don d'in koda Mun kashe shi ya riga da ya bada Order cewar a tada Wannan weapon d'in domin a girgiza shugabannin mu sannan su sa Nigeria cikin firgici da tsoro ! Wannan wani sabon salo ne na neman mulki karfi da yaji , su kuma mutane kamar su MK da suke biye masa duk yayi musu alk'awari zasu samu rabo mai tsoka daga Gare shi shiyasa zuciyar su ta bushe ! Duk wannan bayanan yana cikin files d'in Dad d'ina koda Mun kashe Don BK bamu yi komai ba domin ya wakilta wanda ya fishi had'ari kuma yanzu haka suna Chan a Abuja akwai mutane na guda biyar a cikin su daga nan na samu labarin komai kuma everything is under control for now ! Plans nasu on 1st October zai awku don haka we have only a week to stop them ! Amma kafin nan dole mu tabbatar kar wanda yayi celebrating Independence!!"

Ajiyar zuciya General ya sauk'e ya kalli Don BK dake galabaice yace " Bazamu kashe ka ba ! Har se kaga yanda plans naka da ka shafe shekaru ashirin da y'an kai kana had'awa sun ruguje sannan zaka mutu ! Kisan wulak'anci!!" General yana kai nan ya fice Hydar na biye da shi suka kashe wutan gami da rufe k'ofar.....

Hydar na fitowa ya iske Lana tana tsaye yanda ya barta ,fuska a murtuk'e yace " What now ? " murmushi tayi tace " I just wanna say am sorry? " Ba tare da ya kalleta ba yace " Apology accepted! " murmushi sosai tayi ta mik'a masa hannu tace " Friends?" Kallon hannun yayi sannan ya dubeta ba tare da ya yi shaking natan ba yace " Frndz " sosai hakan ma ya burgeta ta juya tana murmushi Hydar ya juya yana tafiya sannan yayi Murmushi yace " wahalallliya!!😂

A hankali ya bud'e k'ofar ward d'in ya shigo yana fad'in " Har yanzu baki farfado daga kwayar da kika sha bane 😜? Had'e rai Zainab tayi tace " me haka dan Allah yaya! Ni ba y'ar kwaya bace! Kuma ina ka shiga? Se yanzu kaga daman dubani? Gaskiya bakayi ba yaya!"

Azeeza dake gefe tace " Ai ba ke kad'ai ba wata naga har kuka. Ta Fara" tana maganar tana kallon Asy ta gefe ,murguda baki Asy tayi tace " Waye yayi kukan ? Akan wannan uban masifan da jiji da kai Zan yi hawaye ?" Hydar ya yi dariya sosai ya kashe wa Asy ido yayinda Asy ta wani had'e rai. Tana nad'e hannun ta a k'irjin ta, Hydar ya juya Mata baya yace tab!ashe dai ina da fans da yawa harda su y'ar sanda ma!😂

Zainab dake kwance ta buge shi a kafad'a tace " Kai yaya!" Duk suka bushe da dariya Asy ta fice daga d'akin Azeeza ta tab'o Hydar tayi nuni da k'ofa , Murmushi yayi gami da Mik'ewa ya bi bayan ta...................

Jeeddah ja'o🏵️

[10/20, 10:12 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻

🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🎞️1️⃣3️⃣5️⃣

Zaune ya iske ta kan kujera ta lumshe ido tana Murmushi kumatun nan sun ciko kamar funkasau 😜 seda ya k'are Mata kallo sannan yayi murmushi yace

" ya akayi ne Macen fama?!" Murmushin me kike yi? Oh ! Nasani ba se kin fad'a ba ! Tunani na kike ko?" Yana maganan yana kanne Mata ido. Asy bata san lokacin da ta mik'e ba tace " Akan me Zan yi tunanin ka? Kaida kullum fad'a muke da kai! Ni karka dameni ba wani missing naka da nayi!" Tana kai wannan ta mik'e zata fice.

Hydar ya girgiza kai ya sha gaban ta yace " me na b'oyewa kuma? Just say you miss me coz I can see it! Right in ur eyes! " Murmushi Asy tayi sannan tace " Never!! " ta bi gefen shi ta wuce tana dariya ,shima dariyar yayi ya tsaya duba wayar shi da yaji 'karan message , kafin ya d'aga kai Asy har ta fice don haka yayi y'ar dariya yace " I know u missed me !" Ya d'aga gira d'aya sannan ya koma d'akin da Zainab take ya sanar da Uncle Junaid Zai taking morning flight to Nigeria zainab ta had'e rai tace " Haba yaya! Ni gaskiya barin zauna ba se na bika!" Murmushi yayi yace " don't worry dear kuma zaku zo ai , ni d'in Ana nema na ne kiyi hak'uri

. Da kyar Hydar yayi convincing zainab ta yarda zasu je daga baya...................

K'arfe takwas na yamma jirgin su Hydar ya d'aga shi da General, under strict security suka taho da don BK har kasar Nigeria!!

Zaune na hango shi cikin office d'in general sanye da kayan soji abun gwanin burgewa ,kayan yayi matuk'ar masa kyau  murmushi yake sosai haka ma general ga alamu hirar su suke yi , sun dad'e a haka kafin Hydar ya fito daga Office d'in yana tafe amma idon kowa a kan shi ,duk labari ya bazu cewa d'an general ne ya dawo 😂 bai ma wani dad'e a sabon office nashi ba ya fice shima kansa bai Saba ba .............

Yana fita bai zame ko ina ba se wani d'aki wanda babu komai ciki se computers da alama security room na wajen ne , saida ya k'arewa computers d'in kallo sannan yayi gyaran murya ,duk ma'aikatan se harkokin gaban su sukeyi ,firgigit sukayi ganin Hydar duk suka mik'e gami da Sara masa . Rai a bace yace " wannan shine aikin ku? A yayinda duk Mun sa rai kuna aikin ku yadda ya kamata ! Ashe ku kwata kwata sharholiyar ku kuke tafkawa ! Yanzu zaka iya fad'amin lokacin da general ya shigo ?" Mutumin ya girgiza kai yace " we sorry sir!!" Tsaki Hydar yaja yace " You have only one option! Concentrate or put down your ranks and get back to hawking domin ina ganin shi zai fi dacewa da ku !! Kan su a k'asa suka bashi hak'uri , Hydar bai fiye  son damuwa ba yace " Alright then ! Concentrate! Hydar ya gama tab'e taben sa a computern su kansu basu san abunda yayi ba , Don BK yayi appearing a computern guda biyu yace " Kusa min ido akan wannan ! And mind you! If anything goes wrong kunji ni da kyau you'll be shot to

death! " zaro ido d'ayan yayi yace insha Allah hakan ma bazai faru ba! Hydar bai tanka shi ba ya fice abunsa ya barsu duk ciki ya dura ruwa 😂basu san barazana bace.

K'arfe bakwai na dare su Zainab suka iso Nigeria ,direct gidan General aka wuce da su , Hydar ya fita kenan suka iso don haka basu had'u ba Asy se rawar kai ake yi zata ga daddyn ta tun Isar su take manne da jikin daddyn ta abun ya burge su Azeeza sosai General na da kirki shima yana Jan su Zainab a jiki saboda yasan yanzu shine komai nasu sosai sukayi feeling safeguarded a tare da shi..............

Washegari suna zaune a falo su duka harda General se hirar su sukeyi Hydar yayi sallama , jin Muryar sa Zainab ta mik'e da gudu tayi hanyar k'ofa tana dariya , shima da ya ganta dariyar ya Fara gami da rungume ta yace " I missed you dear! Yaya jikin naki? " murmushi ta masa tace " da sauk'i ai na warke " hannun ta ya Kama suka k'arasa cikin falon , kanshi a k'asa ya gaida General ,cike da fara'a ya amsa yace " Ka gama aikin jiya? " Hydar yayi murmushi yace " yes Sir! Oh I mean Dad! " dariya sosai General yayi yace " Allah ya shirye ka soldier!" Shima Hydar dariyar yayi yace " Na samo inda suke planning d'in bomb d'in kuma Mun yi taking cover yanzu haka suna hannu daga su har nuclear weapon d'in ban kwanta ba jiya seda muka tabbatar sun shiga hannu yanzu haka they are detained "

General ya jinjina wa Hydar sosai ganin kwazo da k'ok'arin Hydar! Sannan yaje ya shirya suka fice tare kwata kwata ko kallon inda Asy take bai yi ba hakan yayi mugun sa ta cikin damuwa Azeeza ta gane hakan sosai kawai tayi dariya ta cigaba da wasa da wayar ta................

Hydar na zaune a office nashi yaji an buga k'ofa, "come in!" Ya fad'a ba tare da ya d'ago ba hankalin shi na kan laptop nashi. A hankali ta bud'e kofan ta shigo " Zan iya zama yallabai?" Ta tambaya tana murmushi. Mamaki ne ya Kama shi jin Muryar Asy da sauri ya d'ago kai yace " Yadai macen fama? Me kuma ya kawo ki? Kodai yau ma kin yi missing d'ina ne?" Ya kashe Mata ido , sunkuyar da kanta tayi tana murmushi kafin tace " Kai de kana da matsala! " dariya yayi yana mai rufe system d'in nashi yace " Kedai kawai kice kina missing Soldier!"

Murmushi sosai tayi tace " yes! I missed you! I missed your smile and jiji da kai! Shi yasa na zo ! Kasan wani abu kuwa? Ji nake koda shekaru d'ari Zan kwashe har lokacin dai yanayin da naji lokacin da na Fara ganin ka shi Zan ji ! Shiyasa na zubar da makamai na! " dariya sosai Hydar yayi yace " I knew it! Hey! Tashi mu fita nan wajen is boring " Yana magana yana yamutsa fuska , murmushi tayi itama ta mik'e suka fita...............

Hydar yana driving yayi ajiyar zuciya yace " ina zamu je ne macen fama? Murmushi sosai tayi tana kallon sa kafin tace " Nima ban sani ba Hydar , amma ji nake kamar na shafe tsawon shekaru muna tafiya a haka! " murmushi Hydar yayi ba tare da ya ce komai ba yaci gaba da driving ba tare da yasan inda ya dosa ba💃

Jeeddah ja'o🏵️

[10/20, 10:12 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
136🎞️1️⃣4️⃣0️⃣

IN DEDICATION TO LUVLY SISTERS @UT@R H@JIY@
EN ASY KHALEEL😘

9:00 pm

Hydar na zaune a office nashi still yaji an yi knocking , ba tare da ya d'ago ba yace " come in" yaci gaba da harkar gaban sa se ji yayi ance " All work no play makes jack a dull boy"

Da sauri Hydar ya d'ago karaf idanuwan su suka had'u ya gyara zaman shi yace " Yousuf mainasara???"
Dariya sosai Yusouf Mainasara yayi yace " kana mamaki ne? Toh ai wannan ba wani abun mamaki bane don ka ganni a gaban ka! Nasan tunda na shigo bani da hanyar fita kuma ban zo nan don na fita ba , na kawo kaina ne , kasan me Hydar? Gaba d'aya kai da mutanen ka duk kun riga kun gama da mutane na ,ban ga abunda ya rage min ba,kuma koda baku kashe ni ba mutuwar kawai zan yi the only difference is that idan kun barni Cutar cancer ce zata kashe ni idan kuma na kawo kaina kuma harbi ne da bindiga ko kuma rataya har lahira so bani da zab'i kuma ban yi nadamar abunda na aikata ba! Domin mahaifin ka ya fini kwazo da komai sannan yak'i shiga agenda r mu irin wad'annan mutane barinsu suna numfashi ai babban matsala ce.

Hydar a fusace ya mik'e ya kai masa naushi saida ya dungura daga shi har kujerar sa ,nan Hydar ya zagayo inda yake ya Fara aika masa sak'onni na duka 👊🏽 kamar an aiko shi. Wasu sojoji ne suka banko k'ofar tare da general suka Fara k'ok'arin janye Hydar daga jikin Yousuf mainasara amma kamar chewing gum sam yak'i sake shi. General har ya gaji ya rasa yanda zai yi se ganin Junaid yayi yana k'iran wani layi " Hello kinga Wannan saurayin naki sam ya haukace kiyi magana ko zai Dena pls , come up with something wanda zaisa ya Bari !!" General ya Saki baki jin wanda aka k'ira itace Y'ar sa Asy shi sam bai tsammanin wani abu tsakanin su ba
" Hydar pls stop it!" Kalmar kawai da Asy ta fad'a ta waya ,kuma kalmar da ya dakatar da Hydar daga surfen da yake yiwa Mainasara! Da sauri sojojin suka Janye Mainasara sukayi waje da shi zuwa detention room. Hydar ya d'an daidaita kanshi yace " Ya dai macen fama? Me kuma ya faru?" Kasantuwar Hands free wayar take Asy tace " Ka nutsu mana! This is ur last prep! Kuma ya kawo kanshi dan kanshi mesa zaka yi asarar karfin ka ? Why not save it for something else😉" sosai Hydar yayi murmushi ya karb'e wayar daga Hannun Uncle Junaid ya fice daga Office din , wajen ya rage daga General se Uncle Junaid general yace " Na kasa fahimtar wannan alamarin! Kar ka fad'a min abunda nake tunani shi yake faruwa?" Uncle Junaid ya gyara tsayuwar rigar sa yace " baka ga komai ba! Yaran naka players ne , a wajen aiki basa shiri amma a bayan fagge laila da majnun suke" sosai General yayi dariya yace " toh Allah shi kyauta! Junaid ya amsa da Ameen"

K'arshen tika tika tik! Nasara yace 99 days for d thief nd just a day for d owner! Nothing in this world is worthy of patience ! Rashin hak'uri halaka ne ! Tozarta kai ne ! Shine farkon abunda yake jawo kwadayi da kuma rashin imani da rashin tawakkali it happens in this world ! Brothers don't trust each other gudun wani zai cutar da wani , talaka na tsoron d'an uwansa mai kudi kuma da ace zai aminta da shi se yayi butulci! Mace na kyashin Dan uwanta saboda ya samu , zumunci ya yanke , da dai sauransu a wajen wani ran dan uwansa tamkar na kyashi ne. Allah ka tsare mu da rud'in duniya domin itace babbar halaka! Allah kuma ya bamu Kyakkyawar zuciya tsarkakakkiya ya kuma sa muyi amfani da lessons da muke d'auka. Ina kuma fatan ko da kad'an ne wani ya amfana da abunda na rubuta. ALLAH YASA MU DACE" AMEEN!!

TWO MONTHS LATER!

Da sauri Zainab @ut@r h@jiy@ ta shigo gida tana guna guni se turo baki take , Azeeza na zaune kan carpet tana daka loma 🍛. Kafin ta yi magana ma se ga Hydar ya shigo cikin bak'ar shirt me v neck da wandon soji hannun sa wayoyi ne guda biyu fuskar nan a d'aure yana kallon Zee ita kuwa kai a k'asa ta juya masa baya.

Bai kai ga bud'e baki ba Asy ta mak'ale wuyan shi ta baya ta rad'a masa a kunne " Adai bi a hankali Soldier! " murmushi sosai yayi kafin yace " kinga wannan yarinyar bata ji wlhy I warned her ban son ganin wancan Albino boyfriend d'in nata a k'ofar gida na amma bata ji" a hankali zainab tace " Oooh yaya pls shi fa ba Albino bane kawai farin shi ne haka kuma kai da kana son Aunty Asy waye ya Hana ka naga ma yanzu matar ka ce ita 😏"

Sosai dariya ya kufce wa su Asy harda Azeeza nan zainab ta watsa Mata Harara tace " Tab! Ai wallahy da nice ke ko motsi bazan yi ba ! Yaya Azeeza fa don tsabar samun guri har outing suna fita da Ahmad ni kuma shikenan a Hana ni sakat?"

Hydar don tsabar dariya seda ya zare hannayen Asy daga wuyan shi ya nemi waje ya zauna yana kallon Zee kafin yace " Iyeee??? Ashe dai kanwar tawa ta girma ! Su zee manya ko kunya babu kike cewa na Hana ki sakat don kawai na Hana ki ganin Albino boy naki?" Uhm !! Wai yaya mesa kake haka ne pls shi ba albino bane pls yaya ka samu lokaci ku gana da shi you'll definitely like him " Tab'e baki Hydar yayi yace " Oya je kice yazo ina son ganin shi , and mind you! Idan bai Mun ba Kora shi zan yi daga gidana! " sosai Azeeza take dariya Asy ma haka seda zainab ta fita yace " Macen fama ! Meet me at mah room" yana kai wannan ya wuce upstairs tayi murmushi ta dubi Azeeza dake k'ok'arin kai glass na ruwa bakin ta tace " idan sun shigo suzo falon yayan ki" kai kawai Azeeza ta girgiza Mata Asy tayi murmushi ta haura sama itama.........

Da sallama ta shigo d'akin ya amsa Mata sannan ya d'ago yana k'are Mata kallo from head to toe yace " kin san wani abu kuwa? Nifa ban san mesa na k'ira ki ba😉 " Asy ta k'arasa zuwa inda yake kwance kan gadon ta d'aura hannun ta saman kirjin shi tace " na sani ai! "

janyota yayi jikin shi yace " nasan abu guda! Dat I love you!" Murmushi tayi tace " kai ! You are in control of me  my beloved cos my hrt is careless today let d crazy words say what they want to say" dariya sosai yayi yace " your mood is romantic tonight! Idan na tsaya jin kalaman ki bazan ga Albino in law d'ina ba so ki Adana su nan da anjima kad'an macen fama " yana kai wannan ya manna Mata kiss a goshi yace tashi muje ki tarbi in-law dinki
[10/20, 10:12 AM] +234 701 661 4602: 💻🔫 BURIN FANSA 🔫💻
🔪💔 NA HAUWA ISAH JA'O 💔🔪( 2016)
🔢🎞1️⃣4️⃣6️⃣
🌹FINAL EPISODE 🌹
IN DEDICATION TO LUVLY SISTERS @UT@R H@JIY@
EN ASY KHALEEL😘

Wani had'adden guy na hango zaune a kan kujera ya d'an karkace yana facing zainab se kus kus suke yi , " wlhy kasan yadda zakayi winning zuciyar yaya don he's tough kuma banda gaisuwa kada ka sake magana se in ya baka dama" kai saurayin ya girgiza yana mai murmushi sosai kyau kuwa kamar kwasa yayi.

Hydar da Asy suna fitowa ya tsaya a bakin kofa ya k'are musu kallo se maganganun su sukeyi basu ma san ya iso ba , murmushi Hydar d'in yayi ya kalli Asy yace " perfect match 😉 " dariyar ta ne ya sa su zainab suka d'ago , saurayin ya durk'usa har k'asa ya gaida Hydar, ba yabo ba fallasa ya amsa yana neman wajen zama Asy kuwa ta wuce kitchen don kawo musu tea kasantuwar sanyi ake yi.

A hankali ya dubi Zainab yace " Autar Hajjaju kidan bamu waje I would like to talk in person with your albin....... Bai karasa ba yayi gum da baki zainab ta turo baki tace "yaya mana!"D'auke kai yayi yana dariya sannan ya dubi saurayin yace " Sorry about that, yaya sunan ka ? " Um suna na Othman Omar " kai hydar ya jinjina yayi dariya yace " Bana buk'atar sauran bayanai " kai d'an asalin Gombe state ne , now a medical doctor kuma professional! Mahaifin ka baya a raye se mahaifiya , kana da yaya namiji guda d'aya sannan kuma yanzu haka kana zama ne a gidan ka na Gwagwalada , nasan duk halayen ka from a to z don haka bana bukatar ka sanar da ni all I need to know is How much love you have for my sis and a lokacin da na iso falon nan na riga na gane irin wanne ne so ina so ka bani nan da two hours duk hukuncin da na yanke zainab zata sanar maka." Hydar yana kaiwa nan ya kurbi tea sannan ya mik'e yace " Macen fama zamu wuce masallaci ki shirya mana dinner nida Othman and also Uncle Junaid bazai samu zuwa yau ba so ki mayar da files da na baki. Oh kinga naso na manta da abu guda " just want to remind you! Keep those romantic words secured😉"

Sosai tayi dariya sannan ta kwashe mugs din ta kai ciki

Finally Hydar ya gaji da game d'in da yake yi na sawa zee fargaba ya yarda ya amince zancen Auren ta da Othman haka ma Azeeza da captain Ahmad ( newly recruited soldier)! .......

ALHAMDULILLAH!
My fans am sorry for cutting this short but I think its tym we close the chapter of fansa 😉
Inda nayi kuskure Allah ya yafe min inda kuma nai daidai Allah yasa mu amfana da shi baki d'aya, Masu irin hali na MK kuma Allah yasa su gyara domin butulci ba zai d'aure ba dole akwai ranar kin dillanci.

All credits goes to You
Autar hajiya
Asy khaleel
Mah Namecy JIIDDA BELLO
maman Aiman da Tasleem......

Also to the worlds best friends💞
Rookie kaxs👯
Feedoh y'ar ficika 😘
Ummu Bassam
Teemah Ajiya ( maman farwa) And all humble members of the J JA'O AND R. KAXS GRP !

READERS DIGEST
FEEDOH ND BIEBEE GRP
DANDALIN AUTAR HAJIYA
JIDDAH BELLO NOVELS AND ENTIRE ONLINE HAUSA WRITERS / EXCELLENT WRITERS

Feel free to contact me for any correction if any coz mutum tara yake bai cika goma ba
THANK YOU FANS!!!

Taku har kullum JEEDDAH JA'O🏵️